Fuskar shi na ƙurawa ido bisanin na kai hannuna bisa sajen shi ina shafawa a hankali,lips ɗina na kai bisa na shi na basu wata ƙyaƙyawar sumba kafin na miƙe na fice daga ɗakin ina mai kashe hasken ɗakin.

Part ɗin mu na koma na kwanta,wuraren 2h na farka nayi wanka sannan na tada Hajiya Babba ita ma tayi.
Sai da mu ka shirya tsaf sannan mu ka fito falo,Ameera na biye da mu a nan mu ka tarar da Mami.Jikinta na faɗa ina shirin kuka nan ta shiga bubuga bayana ta na kwantar min da hankali "Ameera je ki tashe da Abban ku ina ga kamar bai tashi ba"cewar Hajiya Babba dan kuwa ta lura ba sa shi da Mami shiyasa ba ta tada shi ba.

Sai Ameera ta kai wajen minti goma sannan Daddy ya farka da wahalalen barcin da ya ke,fuska

kawai ya wanke da baki ya fito saboda tuni lokaci ya ƙure.

Har mota Ameera da Mami suka mana rakiya kafin mai gadi ya buɗe mana get,ba mu yi tafiya sosai ba mu ka kawo EMA transport voyageurs tuni kuwa an fara appel.

Mu na nan tsaye har aka zo da sunan mu,har cikin mota Daddy ya shiga sai da ya ga mun zauna sannan ya fito ya jira aka gama appel motar ta ɓaga zuwa Niamey.
"Allah sauke ku lafiya ya tsare min ke Mimi da sharrin abokai irin su Nabeela"ya faɗi haka ya na mai nufar motar shi,har cikin zuciyar shi ya ke jin kamar ya sauke wani nauyi na nisanta Mimi daga baƙar abokiyarta Nabee.
Ya na tuƙi idon shi na rufe,babu zato ba tsammani ya kaiwa wani tangaraho karo saboda maganin barcin bai sake shi ba.....

*Ku yi haƙuri wlh ban cikin yanayi*🥺🥺
[26/11 à 19:09] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Page 23-24*

Sai da gari ya waye mutane suka farga da motar Daddy wacce tuni madubin gaba ya fashe,ba'a wani ɓata lokaci ba ƴan sanda suka zo tare da miƙa shi asibiti Hamdallah kasancewar ta fi kusa da su.

Taimakon gaggawa aka shiga baiwa Daddy aka cire glass ɗin da ya cake shi ga wuya aka naɗe gun da bandeji‹awani huɗu cur sannan ya farka rumtse ido yayi ganin shi kwance a gadon asibiti a take duk abinda ya faru ya dawo mashi a kai a zuci yace "kenan accident nayi?"

Ya na nan kwance likita ya shigo ya duba shi haɗi da ƙara yi mashi wasu allurai babu jimawa barci ya ɗauke shi,yayinda a cikin barcin ya ke ta mafarkin Mimi.

Ganin Daddy bai dawo ba sam bai tadawa Mami hankali ba,hasali ma Dr Ibrah ta kira suka sha hirar su tamkar wasu masoya.Ba wata hira ba ce sai ta batsa da nunawa junansu sun yi kewar juna nan fah ne Mami ke sanar da shi Daddy bai dawo ba,shiru yayi can yace "kar ace dai shine yayi accident dan ɗazu a wani group na ga an turo wata mota kalar ta shi"da sauri Mami ta dafe

ƙirji ko kafin tace wani abu Dr Ibrah ya kashe kiran hađi da bin didigin ainahin labarin a ƙarshe ya tabbatar da Daddy ne.

Ameera da twins suna falo su na kallo Dr Ibrah ya shigo,cike da ladabi Ameera ta gaishe shi ya amsa tare da cewa "ina Rahman ta ke ?jikin nata da sauƙi?"

"Ta na đakin ta kenan ba ta lafiya?"cewar Ameera "eh wlh tun da ta samu labarin baban ku yayi hađari shikenan ciwonta ya motsa shine na zo na dubata".

Cike da tashin hankali Ameera tace "accident ?yanzu ya na ina?" "Ya na Clinic Hamdallah ungo kuđin adaidaita sai kuje ke da su Twins ku tsaya can kafin mu zo"Ameera na sharar hawaye ta amshi kuđin hađi da jan ƙannanta suka fice .

Murmushi Dr Ibrah yayi ya haura đakin Mami ,a zaune ya tarar da ita tayi tagumi hawaye na zuba a kumcinta,wani irin fincikota yayi ta fađa jikin shi.Halshe ya sa ya na shanye hawayen yace "a kan waccan banza ne kike min asarar hawayen ki?"ta buđa baki da niyyar magana yayi saurin saka nashi.

Sumba ya ke bata ta fita hankali tuni suka fita hayyacin su ,tamkar wasu ma'aurata haka ya tuɓeta ya fara sex da ita sai ihu suke.
Sai da suka yi suka gaji dan kan su kafin su yi wanka,Mami ta shiga kitchen ta samo masu abinci suka ci suka nar kafin su buge da barci.

Da isar Ameera asibiti ba ta wani sha wuya ba suka samu ganin Daddy wanda ke ta sharar barci,har wajen awa biyu da zuwan su amman bai tashi ba.
"Ku zauna nan in tafi gida in đauko mana abinci kar ku fita ko da bakin ƙofa ne kun ji ko?"cewar Ameera kai suka jinjina mata ita kuwa ta fito bakin hanya ta samu adaidaita.

Cike da mamakin ganin motar Dr Ibrah har yanzu bai bar gidan ba komi?ta shiga ciki.
Part đin Mami ta nufa har ta đora hannunta kan handle đin ƙofa sai taji muryar Dr Ibrah ya na cewa "ya ya kika ji kayan aiki ba kamar na mijin ki ba ko?"dariyar duniyanci Mami tayi tace "ai Mu'azam ya fi ka komi kan tsawon kan kauri kawai shi matsalar shi bai san yadda zai sarrafa mace ba ne sannan sai matsalar saurin kawowa"cike da jin haushi Dr Ibrah đin yace "kuma kike

ihu babu ruwana da munafurci bari ki ga na tashi na tafi wancan mai gadin na ku sai baƙin sa idon tsiya wai fah har da ce min yayi ai mai gidan bai nan,ni kuwa na ƙi kula shi"da sauri Ameera ta bar gun ta shiga kitchen jikinta na karkarwa dan kuwa ita ba yarinya ba ce balle ta ƙi fahimtar inda kalaman Dr Ibrah suka nufa.

Abincin ta zuba haɗi da ɗaukar exotic sannan ta fito,kiciɓus suka yi da su Mami wacce ta rako Dr Ibrah.
A ɗan daburce Mami ta kalleta tace "yo ba ki je asibitin ba?"dan dama Dr Ibrah ya gaya mata yadda suka yi,kai Ameera ta girgiza tace "na tafi dawowa nayi ɗaukar abinci" Mami ta ce "toh lafiya kike kuka ko wani abun ne?"kallon mahaifiyarta ta tayi sannan tace "Daddy ne tun zuwan mu bai tashi ba kuma an naɗe mashi wuya"ta ƙarashe maganar ta na fashewa da kuka wata ajiyar zuciya Mami ta saki dan ita azaton ta ko tun ɗazu Ameera ta dawo ta ganta ita da Dr Ibrah.

"Allah baku lafiya ga baki ɗaya ke ma ya kamata ki kula da kan ki sosai ni zan wuce"cewar Dr Ibrah,godiya Mami tayi kafin tace "ni zan koma ɗaki na kwanta ki gaishe shi da jiki"bayan Mami Ameera ta bi da kallo kafin ta fita ta na yiwa Mamin addu'ar shirya tare da alƙawarin ita ma sai ta zama *KARUWAR GIDA* ko dan ta ramawa Daddyn ta😳

***Niamey

Mu na sauka babban birnin Niamey na sake kiran wayar Daddy a karo na barkatai wannan karon kuma a kashe najita,cikin sanyin jiki na kira lambar da ya bani yace in mun sauka na neme shi.

Ashe tuni ma ya na cikin gidan EMA,gaishe shi nayi ina mai nuna mashi Hajiya Babba wacce ke ta masifa an ƙi fiddo mata kayan su daga cikin Boot😂kai ya girgiza a zuci yace "su Hajiya Babba manya ashe har yanzu ta na nan dai yadda na santa"ƙarasawa yayi gun ta ya gaishe ta amsawa tayi ta na mai cigaba da mita .

Har mota ya kai su sannan ya dawo ya fara ɗaukar masu kayan da suka raɓe,sai da ya gama sannan ya zagaya ya zauna seat ɗin drever.

A hanya ya ke ɗan jan mu da hira har mu ka kawo gidan da Daddy yasa aka kama mana haya,a gajiye duk mu ka shiga ciki Alhaji Kamal ya fita nemo mana abinci.
Ko da ya dawo har mun yi wanka mun canza kaya haɗi da yin Sallah Asar,gasasun kaji ne haɗi da frite ya sawo mana sai lemun kwalba.

Hajiya Babba ta baje sai ci ta ke ni kuwa shiru nayi na koma gefe ina tunanin Daddyna ko lafiya

bai ɗaukar kira ita kuwa Mami fushi ni ke da ita dan a mota Hajiya Babba tayi ta faɗa min mugayen halayenta lokacin da suka zauna gida guda haka ba ta tausayin Daddyna.

"Mimi lafiya ?ke ba za ki ci abincin ba?"cewar Alhaji Kamal,Hajiya Babba ta ja baki tace "ta ya za ta ci ta tsaya tunanin Abbanta sai kace wani ɗan yaro duk ta wani damu dan bai kira ba"dariya Alhaji yayi ni kuwa na turo baki gaba cike da jin haushi na nufi ɗakin da mu ka ajiye kaya wanda ya ke ɗauke da matala 3places ta sha shimfiɗa ta alfarma.

A can Maradi kuwa sai wajen sallah magrib ya farka,sannu Ameera ta shiga yi mashi bai amsa ba kawai dai ya sakar mata murmurshi.
Likita ta fita ta kira ya zo ya duba shi "gobe zuwa safe in shaa Allah za'a sallame ka bayan ka biya kuɗin da aka yi ma aiki"cewar Dr ɗin ya na kallon Daddy.

"Na gode sosai da kulawa"cewar Daddy, toilet ya nufa yayi wanka haɗi da alwala.Saloli ya shiga yi tun asubah har magrib ya na nan zaune har aka kira isha'i,bayan ya gama ya juyo ya kalli Ameera yace "Ameera samo min exotic"da toh ta miƙe ta fita zuwa frigon asibitin lemun da ta aje ta ɗauko mashi ya karɓa ya yi Bismillah ya sha.
Bayan yayi Hamdallah da Ubangiji ya ke tambayarta ya aka yi ta sani?babu abinda da ta ɓoye mashi tun daga zuwan Dr Ibrah maganar da taji su na yi ne da Mami kawai a ba ta gaya mashi ba.
Shiru Daddy yayi ya na saurarenta tabbas zargin shi ya zama gaskiya,ta yaya Dr Ibrah zai zo gidan shi bayan duk abinda ya faru tsakanin su?bai ce komi ba sai Twins da ya ƙurawa ido suna sharar barci saboda gajiyar da suka yi.

Washegari tun da safe Dr Ibrah ya sake zowa wai ya zo dubiya ne Amman a zahiri cashe ayar su suke shi da Mami a falo,sai masha'ar su suke.
Daddy kuwa sai da aka sa wayar shi da aka ɗauko daga mota caji yayi masu transfer kafin ya nufo gida Ameera na addu'ar Allah ya toni asirin mahaifiyarta.
Mai gadi na buɗe gate Daddy ya cinno hancin motar shi cikin gidan....
[28/11 à 06:29] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Page 25-26*

Cak Ameera ta tsaya ganin Mami kwance Dr Ibrah na ƙoƙarin saka mata ƙarin ruwa a hannu,bungulin hijabin da ta sanya ya fi komi baiwa Ameera mamaki "yaushe Mami ta fara saka hijab?wai ma miye ya ƙara kawo wannan mutumen..."Daddy ne ya katse mata tunani da cewa "Ameera ja daga bakin ƙofa mana kin tare hanya"cikin ɗakin ta ida shigewa yayinda Twins suka danno kai sannan Daddy.

Kawar da kai gefe yayi kai kace bai gan su a falon ba haka ya wuce part ɗin shi,wanka yayi ya shafa da turare mai ƙamshi sannan ya saka kayan shan iska.
Ko da ya dawo falo Dr Ibrah ya bar gidan "ashe accident aka yi?"cewar Mami ta na ɓata fuska ita ila doli fushi ta ke har yanzu bai tankata ba sai wayar shi da ya ke latsawa ya na karanta text murmurshi kan fuskar shi ```nayi kewar ka ji na ke kamar nayi tsuntsuwa na dawo```😩
```Daddyna shine ko ka kula ni babu kira babu saƙo sai kace wacce aka yi kyauta da ita```😰
```dan Allah kayi min magana da zarar ka kunna waya sannan ka faɗa min dalilin ƙin kula ni har da kashe waya```🥺

Duk text ɗin Mimi ne wasu bai ma samu damar karanta su ba ya danna mata kira,a Shagwaɓe ta ɗaga gami da sallama wata sanyayar ajiyar zuciya Daddy ya sauke jin muryar ta.A zahirin gaskiya tabbas shi ma yayi kewar ta sosai bai taɓa wuni ɗaya bai ji motsinta ba wannan ne karon farko,"Daddyna nayi kewar ka"na faɗa kamar zan yi kuka lumshe ido yayi yace "Mimi da fatan kun sauka lafiya?"da sauri nace "a'a Daddy ni dai tun zuwan mu ban ci komi ba tea ne kawai ni ke sha sai wata ƴar busassar kaza da na ci yanzu"murmurshi mai sauti Daddy yayi wanda har sai da naji shi "kai Mimi kazar ce busassa?to tayi daɗi kuwa?"dariya nayi nace "to ɗan kaɗan dai,wai miyasa ka ƙi nema na koko har ka fara mancewa da ni ?"Daddy yace "wayar ce ta ɓata sai yanzu wanda ya tsinceta ya kawo min"ajiyar zuciya na sauke nace "alhamdullah dama Hajiya Babba tace lafiyar ka lau in bar damuwa da ke ai ba ƙaramin yaro ba n..."dundun da Hajiya Babba ta kai min ne yasa nace "Washhh Daddy😩 Allah wannan tsohuwar so ta ke ta karya maka ni,wani irin duka ta yi min kamar ta bugan guduma"
Daddy bai ce komi ba sai ji yayi Hajiya Babba na magana "ni dai ka turon kuɗin mota na koma wannan sangartatar ƴar ta ka ta hana ni shaƙat sai shegen son jiki ba ta moruwa ga ƴar karen sakuwa sai kace autar mata"dariya Daddy yayi yace "ina kwana Hajiya ?"

"Au !ni ke kiɗina ni ke rawata ko?yanzu ina faɗa maka laifin ƴar ka shine kake wani gaishe ni?"ƙeya Daddy ya ɗan sosa yace "afuwan Hajiyar mu kin san halin Mimi sarai ba ta son wahala ne,kuma please kar a cutar min da ita zan turo kuɗi sai a nema maku ƴar aiki" "da dai ya fi"cewar Hajiya Babba ta na mai miƙo min wayar.

"Daddy ina Mami na?"shiru yayi ya kalli gefen da Mami ta ke kwance ta na barci tuni kuma sérum ɗin ya ƙare,tashi yayi ya cire mata hadi da gyara mata hijab ɗin ta fuskarta ya ɗan tsurawa ido.

Allah ya sani irin son da ya ke yi mata kawai ƴar canzawarta ne bai kwanta mashi a rai ba ga kuma zarginta da ya fara "hello"na faɗa ɗan ƙarfi,lumshe ido yayi yace "umhum!"na turo baki cikin shagwaɓa nace "Daddy shine ka ƙyale ni ?ina Mami?" "Ta na barci"ya bank amsa a takaice,shiru nayi ina tunani dan wannan ba ɗabi'ar Mami ce ba yawan barci a ko wane lokaci ta na ƙoƙarin faranta ran iyalenta shiyasa ta ƙauracewa duk abinda yayi kama da raggonci.
"Mimina zan kira ki an jima"ya na gama faɗa ya kashe ya na sauke wani irin numfashi saboda canjin yanayi da ya fara ji,Ameera wacce ta yiwa Twins wanka ta canza masu kaya ta fito tare da cewa "Daddy mi za'a dafawa tunda Mami na kwance?""ki dafa shinkafa dafa duka sai ki gasa kifi"da "toh"ta amsa ta nufi kitchen Daddy kuwa fita yayi izuwa farfajiyar gidan.

***Bayan 2week

Fadila ce zaune tsakiyar gado ta na danna waya da alamu shart suke ita da Nasir sai Shagwaɓa ta ke zuba mashi,shi kuwa bawan Allah bai cikin nutsuwar shi saboda yayi nadamar kusantar ta tunda har ya ga sakamakon yin haka gun ƙanwar sa.
A ɓangaren su Iyani kuwa doli ta ɗauki ƙaddara ba tare da tayi yunƙurin zubarwa da Fauziya ciki ba,ita kuwa ba ta so haka ba dan a cewarta abun kunya ne ƴan unguwa su ganta da ciki.
Tsangwama kuwa ta na shanta duk in ta gifta Iyani sai ta harareta tamkar idonta za su faɗo,Nabee kuwa ganin ƴar uwarta tayi cikin shege yasa ta ƙara ɗaukar matan tsaro har da zuwa gun wani malami yayi mata laya ta ɗaura ga ƙugu saboda zuwan ɓacin rana kar atai ta samu namijin da zai yi mata ta ƙarfi,amman wannan layar ba za ta taɓa barin namiji kusantar ta ba muddin ta na ga jikinta.

A tsinake ta ke shiryawa cikin wasu fitananun riga da wando wanda suka ɗame mata jiki,wani bungulin hijab ta saka kafin ta rataya bag.
"Iyani zan tafi school sai na dawo"ta na gama faɗa ba ta jira cewar Iyanin ba ta fice, adaidaita sahu ta tsayar da ya ɗauke ta ba su zame ko ina ba sai ƙaton compagnie.

Cike da yauƙi ta nufi office ɗin ba tare da neman izini ba ta ta buɗe ƙofar tare da kutsa kai ciki,da sauri Daddy ya miƙe tsaye ya zagayo sai da ya ƙanƙance ido sannan yace "mi ya ƙara maido ki office ɗina ?"murmurshi tayi tare da cire hijab tace "Washhh Allah na gaji masoyi ka ban ruwan sanyi man"ba ta kai ga ida maganar ba ya ɗauke ta da wani gigitacen mari.
Ihu ta buga tare da yin cikin shi za ta rungume shi yayi wani irin taɗe ta sannan yayi ball da ita,wayar rallonge ya ɗauka ya shiga zuba mata Nabee sai kuka ta ke haɗi da ƙoƙarin tashi amman Daddy na mayar da ita ihunta duk ya karaɗe gun.

PA ne ya shigo ya ceceta,da sauri ta saɓi hijabinta da hannu ta ari na kare😹 "Suraj ka dubi

tantiriyar yarinyar nan wai ta zo har office ɗina neman ra'ayina kwanakin baya ma ta zo na koreta,ban san inda ta samu lambata ba haka ta ke aiko min hotunan ta da mugunyar shiga.Amman da yake ƴar iska ce shine ta sake dawowa"haƙuri PA ya shiga baiwa Daddy ya na mai cewa "uwannan su ne ɓata gari barin su cikin gari ba ƙaramar illa za su yiwa mutane ba"Daddy yace "shiyasa fah na mayar da Mimi Niamey ka san classe ɗin su ɗaya ban san ko miyasa ta ke bibiya ta ba"PA yace "sir wannan da ka ganta ai ka ga *KARUWAR GIDA* saboda idonta a tsatsaye suke"cike da ɓacin rai Daddy ya rufe office ya nufi hanyar gida.

Tun da ya karyo kwanar ya ke jin zuciyar shi na wani matsiyacin bugawa,da mai gadi ya buɗe mashi get ya shiga yayi parking sai murmurshi mai gadi ya ke wanda Daddy bai san na minene ba.

Wani irin sarawa kan Daddy yayi ya na maimaita kalmar "yi da ƙarfi Dr na yauwa da ƙarfi"numfashin shi ne ya tsaya cak na wuccin gadi kafin ya samu zuciyar shi ta fara halbawa da ƙarfi da ƙarfi.
Zaune yayi a falo dafe da zuciya dan ba zai iya ƙarasawa ciki ba,kar ya tai ya ga abinda zai sa zuciyar shi yin bindiga.Ya na nan zaune ya ke jin sautin su tun suna yi da ƙarfi har suka ƙyale,can kamar minti biyar Dr Ibrah ya saɓo Mami zuwa falo babu kaya a jikinsu.
Wani irin sakin Mami Dr Ibrah yayi ya ta faɗi timmm lokacin da idon shi suka sauka kan Mu'azam babban aminin shi,"my lovely kan ka ɗaya da za ka sak...."ragowar maganar ce ta tsaya a maƙoshi sakamakon haɗa ido da suka da Daddy ya zuba mata idon shi da suka yi jawur tsabar ɓacin rai....
[29/11 à 15:22] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Page 27-28*

Tsananin furgice,tashin hankali,rashin zaton faruwar haka ya haifarwa da Mami zubar jini tamkar wacce aka buɗewa pampo kafin wani lokaci tuni lumfashinta ya tsaya cak lokacin da tayi ƙoƙarin tashi tsaye ne juwa ta kayar da ita.
Duk tashin hankalin da Daddy ke ciki ganin Mami cikin wannan halin yasa ya mayar da shi gefe ya nufota ya na kiran sunanta da wannan damar Dr Ibrah ya koma ɗaki ya saka kayan shi tare da ficewa daga gidan.

Duk ruwan da Daddy ke malaya mata bai sa ta farfaɗo ba,ɗakinta ya shiga ya ɗauko mata kayan jikinta bayan ya saka mata ya ciciɓeta zuwa asibiti.

An ɗauki lokaci kafin likita ya fito "masha Allah mun yi nasarar daidaita numfashinta sai da kamar wuya cikin jikinta ya tsaya duba da irin shock da attaque ɗin da suka kawo mata farmaki,zuciyarta ma kingin kaɗan ta buga tsabar tsoro"banda ido babu abinda Daddy ya iya sarrafawa su ma likitan ne ya zubawa wasu,sai da zuciyar shi ta dawo daga suman wucen gadi sannan ya fara jujuya maganar likita bisa lizamin hankali a fili yace "ciki?ciki ne da ita?"cikin tausayi Dr yace "kayi haƙuri bawan Allah nima na so ace ya tsaya duba da shekarun da kuka ɗauka ba ku taɓa samun haihuwa ba,nayi mamaki ma sosai yadda ƙwan halittar ka har iya zama a cikin mahaifarta dan kuwa a wancan karon da na auna ku na ga kamar ma impossible ne saboda ƙarfin ƙwayar hallitar ka amman duba da lamarin na Allah ne shiyasa ban yi décourager ɗin ku ba"

Idon Daddy ne suka rikiɗa suka jawur kamar garwashin wuta,shi sam ya ma manta da ya taɓa zuwa wannan asibitin tun shekarun baya da suka wuce to wai mi ma ke faruwa?

Cikin ruɗani yace "Dr wannan shine ciki na wajen huɗu da ta samu amman uwancan duk da ta haife su"ido Dr ya zaro yace "kuma da kai?"kallon ban gane ba Daddy yayi masjid sai yayi saurin cewa "ina nufin kuma kai ne uban cikin na gaske?"

"Daram!dam!dimmm"haka zuciyar Daddy ta buga,yayinda yawun bakin shi suka kafe ƙwaƙwalwar shi ta daina tunani kafin wani lokaci zuciyar shi ta tsaya cak samakon hasaso abinda ya ke fatan ko a mafarki ne ba zai so ace hakan ta faru ba.

*Wasu shekarun baya da suka shuɗe...*

CEG3 makaranta ce da ke jamhuriyar Niger a garin Maradi,makarantar ta kasance ta ɗaya fannin ƙoƙari da hazaƙa a duk makarantun gwamnati da ke Maradi.
Ɗalibai ne zaune matasa ƴan 4em duk kowanensu sanye ya ke da uniforme,a tsarin classe ɗin 4em mafi akasari matasa ne sabbin balaga saboda a ƙiyasi ƴan 13 zuwa 15years ne.
Gungun students kawai kake gani kowa da abinda ya dame shi,wasu na cin abinci wasu na danna wayar hannu yayinda wasu ke hira.

"Yauwa yanzu abinda za'a yi kowa ya zo ya faɗa mana ra'ayinsa idan ya girma aikin mi zai yi"cewar wani ɗan matashin yaro mai suna Hafiz,nan fah kowa ya shiga faɗin ra'ayinsa haɗi da hujja wasu sun zaɓi koyarwa,wasu aikin soja,masu son kuɗi sun zaɓi aikin ɗan sanda dan karɓar cin hanci.

Hafiz ya dubi Mu'azam yace "ku biyu ya rage ku faɗi ra'ayin ku kai mi kake son zama?"murmurshi Mu'azam yayi yace "ina son na zama ɗan kasuwa nayi kuɗi na gina manyan

gidaje,na sayi motoci dayawa ta yadda zan auri mata huɗu tsalatsala masu kyau "dukansu dariya suka yi dan kuwa kusan kowa ya san yadda Mu'azam ke son yin aure tun da ƙananun shekarunsa saboda ya na da yawan sha'awa.
Ibrahim shine kawai bai faɗi ra'ayinsa ba hakan yasa yace "ku tsaya-ku tsaya dariyar ta isa haka nan a bari na faɗi nawa nima"duk ƙyalewa suka yi suka zuba mashi ido.

Sai da ya gyara zama sannan yace "ni kuma likitan mata ni ke son zama,saboda na rinƙa kallon mata yadda ni ke so in yau na ga baƙa gobe fara zan gani daga nan nima sai nayi profiter eh yane"ihu suka kwashe da shi wasu na sake zuzuta shi yayinda Mu'azam ya kai mashi dukan wasa dan sun fi kusa duk a cikin délégation ɗin.

"Ɗan iska in mutane suka gane ai sai a kore ka"cewar Mu'azam, Ibrahim yayi dariya yace "ai shi Dr Ibrah ya na da ilimi da wayo ba zai yi yadda za'a gano shi ba ƴan ƙauye kawai zan rinƙa eh yane" Mu'azam yace "ku na ji fah wai Dr Ibrah hhh shi har ya ga ya zama likitan hhh"nan aka shiga yiwa Ibrahim dariya ana ce mashi Dr Ibrah ashe wannan abu yayi mashi ciwo sai ya ga kamar da gayya Mu'azam ɗin yasa yin haka collègues sun dare shi.

Cikin fushi ya miƙe ya fice ya bar class ɗin,da sauri Mu'azam ya bi bayansa ya na kiran sunan shi amman ya ƙi ko da juyowa ne balle ya tsaya.Da gudu ya sha gaban shi tunkuɗe shi Ibrahim yayi ya wuce ya bar Mu'azam da mamaki.

Washegari da suka dawo école sai students suke kiran Ibrahim da Dr Ibrah to fah shikenan sunan ya bi shi tun ya na faɗa da jin haushi har ya haƙura amman har yanzu ba su shirya da Mu'azam ba.

A gajiye ya shiga gidan ya na dab da shiga ɗakin shi ya ji muryar Hajiya Babba na cewa "yau kuma lafiya na ga sai ɓata fuska kake kuma ko gaishe ni ba za'a yi ba?"ƙeya ya ɗan sosa yace "a gajiye ni ke wlh ina sauri naje na kwanta ne"cewar Mu'azam Hajiya Babba ba ta ce komi ba sai kayan Munawara da ta ke kwashewa kan igiyar shanya.

Mu'azam na shiga ɗaki ya haye ƴar sofar shi,tunanin canzawar Ibrahim ya ke son yi tare da nemo mafita amman abu ya sauya salo sakamakon ƙugi da marar shi ta ke.
Dafe marar yayi ya furta "ya Allah!"a zuci kuwa cewa ya ke "ƙila wannan shine silar mutuwata ta yaya zan jure wannan muguwar sha'awar a ƴan ƙanƙanan shekaruna?banda kuɗi balle in ce zan yi aure,to wace ce ma za ta aure ni ?"huci ya furzar tare yunƙurawa ya tashi.

Dala biyar ya lalabo a aljihu tare da fita waje ya leƙa ya aiki wani yaro ya sawo mashi ƙanƙara,yaron na miƙo mashi ya buga ƙanƙarar ga bango sannan ya shige ɗaki.

Cikin wani ƙyale ya saka ƙanƙarar ya fara dannawa ga mararsa,a hankali ya ke fitar da numfashin wahala a sannu ciwon ya ke ragewa can barci ya ɗauke shi.

Sai wuraren ƙarfe biyun rana ya farka wandon shi duk ya ɓace da sperm saboda mafarkin da yayi,bokiti ya cika ya je yayi wankan tsarki hadi da yin na sabulu a ƙarshe ya wanke wandon.

Doguwar riga ya saka ya fito daga banɗaki,alwala ya ɗaura kafin ya wuce masallaci.
Ya na dawowa ya tarar da Munawara zaune a ɗakin shi ta na jiran sa,cikin sangarta tace "ya Mu'az tun ɗazu ni ke jiran ka kazo mu ci abinci"bai ce komi ba ya zauna hadi da buɗe abincin da ta kawo masu.
Bismillah yayi ya fara ci ita ma sai ta saka hannunta,"Ya Mu'az albishirin ka"ɗagowa yayi kalleta ganin sai murmurshi ta ke zubawa "ya aka yi ne?"sai da ta ɓoye fuskarta tace "dama ɗan gidan Alhaji Abubakar ne yace ya na sona zai aure ni sai mu tafi Makka "shiru yayi ya na kallonta yarinyar duka ba za ta wuce 12year ba amman murna ta ke za ta yi aure.

"Yaushe ya gaya maki haka?kuma kin tabbata dagaske ya ke?"cewar Mu'azam kafin Munawara tayi magana suka jiyo muryar Alhaji Abubakar da sauri Mu'azam ya fita ya na amsa sallamar saboda duk unguwar Alhaji Abubakar ya fi su kuɗi sannan mutumen kirki ne tun rasuwar mahaifin su shi ya ke aiko masu da abinci duk wata.

Cikin girmamawa ya gaishe shi hadi da yi mashi iso gun Hajiya Babba,har Mu'azam zai fita Alhaji yace "dawo ka zauna yaron kirki "zaunawa Mu'azam yayi.

Nan Alhaji yayi gyaran murya tare da gaya masu abinda ya ke tafe da shi dangane da auren Munawara da yaron wajen shi Kamal ke so, Hajiya Babba tayi murmurshi tace "ai Alhaji duk ƴaƴan ka ne duk yadda kayi daidai ne,ko yau kace za'a ɗaura ni ban ga wata matsala ba tunda da kai da kaya duk mallakar wuya ne".

Sosai Alhaji yayi godiya ya dubi Mu'azam yace "ya karatun har yanzu ka na nan kan bakar ka na son karantar business ko yaya ?"kai Mu'azam ya ɗaga yace "eh in shaa Allah" "ok babu matsala gobe ka zo ka same ni tun da ba'a makaranta sai mu tattauna ka ga za ka iya farawa tun yanzu ta yadda a gaba ba za ka ji wahalar shi ba"godiya Mu'azam yayi.

***Bayan 1week

Hajiya Babba ta gayyato dangin mahaifin su Mu'azam suka tarbi lefen Munawara,dukan su sun yaba inda kuma a nan take aka ɗaura aure biki kuma sai zuwa gaba.
Ɓangaren Mu'azam kuwa tuni ya fara kasuwanci wanda Alhaji ya ɗora shi a kai,a kullum in ya taso daga school shago ya ke wucewa yayinda kuma weekend ya ke zuwa da safe tuni cikin ƙanƙanan lokaci Mu'azam ya fara canzawa yayinda shagon da Alhaji ya bashi ya ƙara bunƙasa.

Ganin Mu'azam ya sayi babur shine yasa Ibrahim saukowa daga dokin gaba,nan fah suka shirya inda a kullum Mu'azam sai ya je gidan su Ibrahim ɗaukar shi sannan su wuce school.

Tafe ta ke ta na yauƙi irin na ƴan matan zamani sai wani karairaya take ta na juya ƙugu,cak Mu'azam ya tsaya daga tuƙin da ya ke ya ƙura mata ido ta miror har ta kawo daf da su.

"Am ƴan mata sannu"ya samu bakin shi da furtawa,tsayawa Rahama tayi tare da dafe ƙugu tayi wani fari da ido wanda ya sa zuciyar Mu'azam da gangar jikinsa amsawa.

"Ka tsayar da ni malam ina sauri ne"ta faɗa cikin dadaɗar murya wacce Mu'azam yaji duk duniya babu muryar da ta kai ta ta daɗi "dan Allah in ba za ki damu ba ina son ki ban lambar wayar ki"wani kallo tayi mashi irin na tara saura kwabo.

Dr Ibrah yace "please ƴan mata ki taimakawa abokina mana ganin ki kawai ya sa duk ya fita hayyacin shi,in kin ƙi ba shi ƙila ya some min nan"ya ida maganar cikin raha wanda hakan yasa ta yin murmushi haɗi da zayyano mashi numberta.

"Sunan jaruma?"cewar Mu'azam "Rahamatullah"ta bashi amsa.....
[02/12 à 12:29] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*29-30*

Tunda Mu'azam ya gamu da Rahma ya ɗauki son duniya ya ɗora mata,gabaɗaya hankalin shi na kanta komi ya samu Rahma dai tsabar son da ya ke yi mata ya sa duk wani abu da ya shafi harafi mai *R* ya ke son shi.

Tuni sunanta ya je gun Hajiya Babba babu kunya haka zai zauna yayi ta bata labarin Rahama,Munawara kuwa kullum cikin tsokanar shi ta ke ta kan ce duk ranar da Rahama tace ba ta son shi daga ranar gidan mahaukata za su kai shi.

Ɓangaren Rahama kuwa ba wani sosai ta ke son Mu'azam ba dan ita tafi son namiji kalar fatar ta wato fari,sai irin yadda ya ke yi mata hidima yasa ta bashi wani gurbi a zuciyar ta .

Cikin masifa Ishalle ta ɗaga labulen ɗakin tace "ke Rahamu uwar mi kike yi da har yanzu ba ki fito ba?ko ba ki ji tun ɗazu aka aiko Mu'azu na waje ya na kiran ki ba?"

"Kimtsawa ne ni ke yi tashina daga barci kenan,amman tsabar jaraba har ya ƙumo sammako ya zo mtsw"ta ja tsaki "to zauna nan dan ubanki garin kallon ruwa kwaɗo yayi maki ƙafa kaf samarin ki akwai tamkar shi?ina ce katifar da ta ke sa ki ranar barci shi ya saya maki ita ko?"Rahama ta turo baki tace "kai anty abun kuma har da gori dan ya saya min katifa?"tsuki Ishalle tayi ta saki labulen direct ƙofar gida ta leƙa ta cewa Mu'azam "Bismillah shigo mana ka tsaya waje kamar wani baƙo"kai Mu'azam ya sosa yace "antyn mu ina kwana?"tace "lafiya lau wuce mana ta na cikin ɗaki"babu muso Mu'azam ya nufi ɗakin Rahama.

Ta na ƙoƙarin saka riga ya shigo bakin shi ɗauke da sallama,da sauri Rahama ta wawuri hijab ta saka a birkice ma ya ke.
Murmushi Mu'azam yayi ya na kokowa da numfashin shi saboda rabin breast ɗin ta da ya gani ta sama farar bra ɗin jikin ta.

Cikin masifa tace "Mu'az miye haka sabida Allah in fah ka tarar da ni ciki mugun hali?amman ai ka ma riga ka gani"ta faɗa ta na turo baki hadi da juya mashi baya.

"Kiyi haƙuri babyna anty tace na shigo ai"ya faɗa cikin kalar tausayi,"shine dan tace ka shigo sai ka biye mata ko?"ta faɗa tare da juyowa ta watsa mashi harara.

Murmushi yayi yace "baby ni kike harare kuma?" Ta bashi amsa da "eh ɗin ai kai ne minene na zowa tun da safe ?"

"Baby sabuwar waya na saya maki shiyasa nace bari na biyo na kawo maki tun jiya na saye ta amman nace bari har na gani in ba ta dawata matsala sai na kawo maki"Mu'azam ya faɗa tare da miƙo mata waya sabuwa dal a kwali.

Har ƙasan zuciyar ta taji daɗin haka sai dai ta ƙi nunawa a fuska sai ma kumbure-kumbure da ta ke yi,cikin rashin jin daɗin sauyin na ta yace "dan Allah baby kiyi haƙuri Allah ba zan sake ba,karɓi ki duba ki gani Allah sa za ta burge ki"ya ida maganar da ɗan murmurshi.

Karɓa tayi ta fiddo ta,tecno ce Spark 5,tsabar daɗi ba ta san lokacin da murmurshi ya suɓuce mata ba.
Mu'azam kuwa bawan Allah wata irin ajiyar zuciya ya sauke ganin murmurshi kan fuskar Rahama.

Tsayawa tayi ta na kallon shi "mi kake ma murmurshi?"amsa ya bata "saboda ganin ki cikin walwala"wani tausayin shi ne ta ji yayinda zuciyarta ta shiga bugawa da ɗan ƙarfi "tabbas Mu'azam shine masoyin gaskiya"ta faɗa a zuci idonta na cika da ƙwalla.

"Ina son ka Mu'az"ta faɗa hawaye na zubowa a kumcinta,wani girrrr ya ji haɗi da yarrr a take kuma tsikar jikinsa ta miƙe yau ne karon farko da ta taɓa faɗa mashi kalmar so.

Shi ma bai san lokacin da hawayen suka zubo mashi ba,ya duƙa yayi sujada shukur ita kuwa dariyar shi ta shiga yi ganin yadda ya ke ta yiwa Allah godiya da ya gwada mashi wannan rana.

Ishalle da ke bakin ƙofa laɓe duk ta na jin komi ta murmursa ta na mai barin gun,sallama Mu'azam yayi mata ya wuce shago.

Ya na zuwa ya tarar da Dr Ibrah zaune shi da wani yaron da suke gudanar da sana'ar tare "sai yanzu ka tawo?"cewar Ibrah ya na mai kallon Mu'azam wanda ke tangale babur.

"Eh wlh ka ga na daɗe ko?gidan su baby na biya  ya ne da fatan ka tashi lafiya?"cewar Mu'azam ya na mai baiwa Ibrah hannu wanda yayi kicin-kicin da fuska jin ya ambaci sunan Rahama.

"Lafiya kake wani cin magani?"Mu'azam ya tambaye shi "ban sani ba,kai shikenan wannan yarinyar ta maida ka ɗan ƙaramin mahaukaci komi Rahama sai kace wata autar mata mtws ni ban ga ma abinda ka gani a jikin ta ba da har kake rawar jiki a kanta"Ibrah ke magana cikin tsantsar fushi da kishi.

"To ni dai ina son ta a haka kai ma ya kamata ka so duk abinda ni ke so"Mu'azam ya faɗa cikin rashin jin daɗin abinda abokin nashi ya faɗa a kan Rahama.

Baki Ibrah ya taɓe yace "can ku ƙarata kai da kaji za ka iya,ni tsohuwar wayar ka na zo karɓa tun da jiya ka sayi sabuwa" sosai ƙeya Mu'azam yayi yace "ai Rahama na saya ma ita shiyasa ma ka ga na daɗe ban zo shago ba can na tafi na kai mata"waro ido Ibrah yayi yace "la'ilah

illallah wayar 95.000f ɗin ce ka baiwa wata ƙatuwar banza Mu'azam kan ka ɗaya kuw..."hannu ya ɗaga mashi yace "Ibrah ya isa haka kar ka ƙara cewa Rahama ƙatuwa saboda duk fafutuka da neman ni ke yi domin ita ni ke yin su dan haka zan iya mallakawa Rahama duk abinda na mallaka"cike da fushi Ibrah ya bar gun.

Wunin ranar haka Mu'azam yayi shi a jagule dan sosai ya ke son abokinsa amman ko kaɗan bai kamo ƙafar Rahama ba, murmurshi yayi tuna manyan breast ɗin ta yammm haka jikinsa yayi tare da jin son yin aure ya taso mashi.

Sai marice ya koma gida inda ya tarar ana ta shirye-shiryen bikin Munawara wanda ya rage kwana biyu kacal,ɗakin shi ya buɗe ya aje kayan da ya shigo sannan ya shiga banɗaki yayi wanka.
A tsanake ya ke shirinsa inda ya saka wasu fararen kaya uwanda suka yi masifar karɓar sa,in ka ga Mu'azam za ka ɗauka ya kai 25years.
Turare ya saka ya buɗe ledar da ya shigo ita ya fitar da na shi sannan ya ƙulle,ya na ƙoƙarin fita yaji muryar Hajiya Babba "ina zuwa kuma yanzu daga shigowar ka,?"waigowa yayi ya gaishe ta sannan yace "zan kaiwa Rahama kayan shigar biki ne"Hajiya Babba ba tace komi ba.

***GIDAN ALHAJI

"Alhaji aure-auren nan ya isa haka,yawan auren nan ba shi zai sa ka samu abinda Allah bai nufa za ka samu ba"wata ƴar datijuwa ke faɗar haka yayinda shi kuma Alhajin da ta ke yiwa magana ya rabka uban tagumi.
Can ya ɗago ya dube ta yace "ki bar wannan zancen dan tuni an ɗaura yanzu haka yau bayan sallah isha'i amarya za ta shigo"ya na gama faɗar haka ya miƙe tsaye ya fito babban falo yayinda Hajiya ke take masa baya.

Samari ne a ƙalla sun kai ashirin da wani abu,duk rusunawa su ka yi su na gaishe da mahaifinsu bai amsa ba sai da ya zauna kan wata farar kujera wacce ta banbanta da ta cikin falon sannan yace "lafiya lau na ke,na sa an tara ku ne a nan dan na shaida maku yau za'a kawo sabuwar tantin ku ina son ku buɗe kunnuwan ku da kyau duk wanda yayi mata rashin kunya akan auren uwar sa"duk sunne kai suka yi Ma'aruf wanda shine babban su kuma ba zai wuce 34years ba yace "auren kuma again?ina roƙon Allah ya sa alkhairi ya sa kuma wannan shine na ƙarshe ya cika ma burin ka"murmurshi kan fuskar Alhaji yace "amen ɗan arziki"Hajiya kuwa ji tayi kamar taje ta maƙure Ɗan na ta dan kuwa kaf cikin yaran shi kawai ke son abinda Alhaji ke so.

Dare na yi kuwa ƴan kan amarya suka zo tun daga Agadez suka kawota,yarinya ce sharaf ƴar duma-duma mai jini a jiki kallo ɗaya za ka yi mata ka san taji Addini duba da yanayin shigarta ba irin yadda amaren zamani suke caɓa kwalliya ba,a goshinta kuma ƙaton tabo ne baƙi ƙirin na sallah.

Alhaji cike da zumuɗi ya gabatar da duk abinda Shari'a ta gindiya tambayoyin da yayi mata na hukunce-hukuncen sallah da sauran su ras ta bashi amsar su.
A slow ya dinga binta har ya mayar da ita cikakkar mace,azaba kam ta sha ta, Alhaji da kan shi ya gasa ta ita kuma sai noƙewa ta ke yi....

**

Cike da murna Rahama ke buɗa kayan da Mu'azam ya kawo mata har kala uku,farar shadda ta shigar safe, lèche na shigar rana sai lafaya ta kan amarya.
Ishalle sai yaba kayan ta ke can tace "ya kamata azo kuma ayi bikin ku kafin ƴan baƙin ciki su kutso kai,kawai ki ce mashi ya turo magabatan shi"dariya Rahama tayi tace "toh ai sai gobe ne zai gabatar da Ni ga danginsa sannan kuma ai sai mun tafi ƙauye ya gaido su Inna"(Ishalle ba ta haihuwa shiyasa ta ɗauko ƙanwarta Rahama daga ƙauye wajen iyayenta,kishiyarta ɗaya sai dai ba gida guda suke ba wannan kenan)

Ranar biki Rahama ta tsantsara ado suka tafi ita da Ishalle,sosai kuwa suka samu tarba mai kyau gun Hajiya Babba sai nan-nan ta ke yi da su.
Dangin Abban su ma sosai suka yaba da Rahama ita kuwa sai sunne kai ta ke,Gift ɗin da ta kawowa Munawara sai kowa yayi san Barka dan kuwa sai da ta danne zuciyar ta tayi mata sayayya irin ta amare.

Da dadare a ka kai amarya gidan surukanta wanda ya ke nan cikin unguwa,Mu'azam kuwa sosai ya ke murna dan kawu Tanimi yace in shaa Allah shi ma in ya shirya za su je nema masa auren Rahama.....
[03/12 à 09:18] Cham~rose💞: *KARUWAR GIDA*

*LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Après chaque prière*

(1)أَسْتَغْفِرُ اللَّهَ(2)اللَّهُمَّ أَنْتَ السَّلاَمُ، وَمِنْكَ السَّلاَمُ، تَبَارَكْتَ يَا ذَا الْجَلاَلِ وَالإِكْرَامِ

Je demande pardon à Allah [trois fois]. Ô Seigneur ! Tu es la Paix et la paix vient de Toi. Béni sois-Tu, ô Digne de glorification et de munificence. »

Muslim 1/414.

*JUMMA'A MUBARAK MES FANS*🕌

*PAGE 31-32*

Cikin ikon Allah an kai lefe gidan su Rahamatullah bayan Mu'azam ya je har ƙauyen su ya gaishe da iyayen ta.
Ba wani saka dogon lokaci ba wata biyu ne kacal,tuni Mu'azam ya fara shirye-shirye ɗakin Hajiya Babba aka gyara wanda ya ke cikin da falo ita kuma ta koma ɗakin shi mai ciki ɗaya.

Abotar su Mu'azam kuwa ta ɗan rage ƙarfi shi da Ibrah duk da sun shirya amman tuni ya gane da Ibrah ya na hassadar shi ne da ƙyashin abun hannun shi.
Munawara babu yadda ba ta yi da Kamal su tsaya har ayi bikin Mu'azam ba amman ya ƙiya a ƙarshe da ya ga za ta kawo mashi cikas yayi mata gami da Hajiya Babba ita kuwa ta shiga yi mata faɗa a ƙarshe ta ɗirka mata ɗan karan duka da ciwon jiki da birdin tsamanga Munawara ta isa Saudiyya tare da ƙudirin ita da zuwa Niger sai kuwa in gawarta za'a kawo tunda ba ƙaunarta Hajiya Babba ke yi ba😆

***Bayan wata biyu

Tuni su Rahama an zama amare,zalama gun Mu'azam kuwa ba'a magana ɗaya rana sai ya nemeta fiye da biyar tun ta na kuka har ta saba sai ya zamana har ta fi mai kora shafawa dan wani sa'in ya na shago za ta kiran shi ta aza mashi kuka sai ya dawo gida ya yi mata abun😆

Cikin zumɓurar baki Rahama ta shiga tuƙa tuwon ta na gunguni tare da zagin Hajiya Babba ƙasa-ƙasa ita da ta sa a yi tuwon laushi,cikin yanayin rashin jin daɗin rashin kunyar da Rahama ta tsiro Hajiya Babba ta dube ta tace "Rahamu yanzu haka ake tuƙa tuwo garin ku?duk kin bi kin ɓata madafa da gari kuma tuwon ki na ganin ya na ƙulalai shine kike zuba gari dayawa?to bani in yi kaya na tun farko sai da nace ku yi girkin ku in yi nawa"

Miƙewa Rahama tayi ta baiwa Hajiya Babba wuri,bakin pampo taje ta wanke hannunta ta shige

ɗaki zaunawa tayi ta kalli baƙuwarta wato ƙawarta Rahama mai irin sunanta tace "wlh na gaji waccan baƙar tsohuwar ta sa ni yi mata ƙaddararen tuwo kiji fah da rana tsaka a saka ni girgizar jiki"
"Innalillahi yanzu takwara uwar mijin ta ki ce tsohuwar banza?"to kiyi saurin tuba ga Allah domin duk wacce ta haifa maka miji ta gama maka komi a duniya "wani uban tsuki ta ja tace "dallah kar ki kawo min ƙabli da ba'adi ke a ko ina sai kin nuna ke ustaziya ce tai can ki zauna ke uwar mijin na ki tayi ta juya ki,shi kuma mijin ki riƙa goya shi iyakar biyayya wai na ga kwanaki har wani duƙawa kike dan za ki miƙa mashi makuli mota kawai salon ya raina ki"

Ita dai ba ta ce komi ba dan ta riga da ta san namsake ɗinta babu abinda ta saka a gaba sai duniya,sallama tayi mata ta yi tafiyarta.

Dare nayi Mu'azam ya dawo,kunkume fuska Rahama tayi shi kuwa bawan Allah duk ya susuce ya shiga tambayarta lafiya buɗar bakinta sai cewa tayi "ai Hajiyar ka ce ta zage ni wai ƴar ƙauye ban iya girki ba,kuma fah ina tsaka da girki ta karɓe wai ai Ɗanta ya yo cefanen shiyasa ma ban yi girkin dare ba kuma ni yanzu yunwa ni ke ji"

Shiru Mu'azam yayi ya na ta juya zancen can dai yace "ina zuwa"ya faɗa tare da fita ya ja babur.
Gasasun kaji da frite ya sawo,sai da ya kaiwa Hajiya Babba na ta sannan ya wuce part ɗin su.
Cike da murna Rahama ta fara cin kajin a zuci kuma ta na kitsa yadda za'a yi ta haɗa tugun da zai sa su bar gidan.

***2years later

Arzikin Mu'azam ya buƙansa sosai dan har yayi na shi jarin yanzu kan ƙafafun shi ya ke tsaye daram,matsalar shi ɗaya ita ce rigimar Rahama kullum da sabuwar fitinar da ta ke kawo mashi yanzu ita kuma Hajiya Babba ta matsa doli sai ya ƙara aure saboda har yanzu Rahama ko ɓatan wata ba tayi ba.

Ɓangaren karatu kuma BEPC kawai Mu'azam ya ke da daga nan kuma ya tattara su ya maida gefe,yayinda Ibrah tuni ya fara karantar karatun likitanci yanzu haka ya na cikin shekara ta biyu.

Kuka Rahama ke yi wiwi kamar ranta zai fita jin wai kishiya za a yi mata,cikin ɗaukar shawarar da takwararta ta bata ta dubi Mu'azam tace "kafin kayi auren sai ka shirya mu fara zuwa asibiti

tukunna a san daga ina ne matsalar ta ke"bai wani damu ba ya amince.

Da zuwan su aka gwada su likita ya tabbatar da duka lafiyar su lau matsala ɗaya ce shine kamar ƙwan haihuwar Mu'azam ya fi ƙarfin ƙwan hallitar Rahama maimakon in sun gamu suyi fécondé sai ya ƙona shi.Cikin dubaru na likitoci ya shiga kwantar masu da hankali sannan yace su dage da addu'a duk da su na da 1% na chance amman lamarin Allah sai shi.

Wannan batu sam bai kwantawa Hajiya Babba ba hakan yasa ta fara neman masu maganin gargajiya a ƙarshe dai sai ta gayyato wani malami kwanan shi bakwai a gidan su ya na aikin shi. Jungum suka yi suna sauraren malam wanda ya ke ta yin murmushi can yace "tabbas akwai arzikin ƴaƴa amman da alamu duk mata sannan hakan za ta faru ne in kun dage da roƙon Allah ku yawaita yin saraka sannan mabuɗin arzikin ku shine ɗaukar Maraya ku ingata rayuwar shi"

"Maraya?ina za mu samu Maraya kuma malam?"cewar Mu'azam "gidan marayu za ku je ku yi adopter ɗin sabuwar haihuwa saboda ita ɗin haske ce tamkar tauraruwa yayin ɗaukar ta za ta canyara kuka ne tamkar lokacin ne aka fiddota daga cikin cikin mahaifiyar ta"malam ya faɗa ya na murmurshi "malam kuma doli sai mace?"Mu'azam ya faɗa dan ya fara ganin abun kamar an kaucewa hanya.

Tsawa Hajiya Babba ta daka mashi tace "ka fi shi sanin aikin shi ne?" Malam yace "istakhara nayi in kuma ka na so kai ma za ka iya yi,tabbas a mafarkina mace na gani haske ya luluɓeta"

Da sauri Mu'azam yace "malam bani karatun istahara ɗin"

Malam yace to ga addu'ar kamar haka:
اللَّهُمَّ إِنِّي أَسْتَخِيـرُكَ بِعِلْمَكَ، وَأسْتَقْدِرُكَ بِقُدْرَتِكَ، وَأَسْأَلُكَ مِنْ فَضْلِكَ الْعَظِيمِ، فَإِنَّكَ تَقْدِرُ وَلَا أَقْدِرُ، وَتَعْلَمُ وَلَا أَعْلَمُ، وَأَنْتَ عَلاَّمُ الْغُيُوبِ،
اللَّهُمَّ إِنْ كُنْتَ تَعْلَمُ أَنَّ هَذَا الأَمْرَ (وَيُسَمِّي حَاجَتَه) خَيْرٌ
لِي فِي دِينِي وَمَعَاشِي وَعَاقِبَةِ أَمْرِي، فَاقْدُرْهُ لِي وَيَسِّرْهُ لِي ثُمَّ بَارِكْ لِي فِيهِ، وَإِنْ كُنْتَ تَعْلَمُ أَنَّ هَذَا الأَمْرَ شَرٌّ لِي فِي دِينِي وَمَعَاشِي وَعَاقِبَةِ
أَمْرِي، فَاصْرِفْهُ عَنِّي وَاصْرِفْنِي عَنْهُ وَاقْدُرْ لِيَ الْخَيْرَ حَيْثُ كَانَ ثُمَّ أَرْضِنِي بِهِ

Godiya Mu'azam yayi sannan Hajiya Babba ta sallami malam.
Dare na yi Mu'azam yayi raka'a biyu sannan ya karanto addu'a da malam ya bashi yayi tawasli da Allah tare da miƙa dukan yarda shi.

***GIDAN ALHAJI

Dr Ma'aruf ne sanye da kayan likitoci,idon shi manne da farin glass hankali tashe ya shigo gidan.
Kallon Abban nasa yayi yace "Abba doli sai an tafi asibiti ka yarda da ni dan Allah wlh ba za'a samu matsalar komi ba"cikin yarda da Ɗan na shi ya tallabo Agaishat wacce ta jigata saboda zafin naƙuda mota ya sakata tare da ɗaukar kayan haihuwa suka wuce asibiti.

Allurar naƙuda Dr Ma'aruf yayi mata sai addu'a ya ke yi Allah sa matan biyu su haifu lokaci ɗaya,waccan ɗayar ta fara nishi da sauri ya tafi ya karɓi haihuwar ta cikin ikon Allah ko minti biyu ba'a yi Agaishat ma ta haihu.
Bisa gado ya ɗora jariran wanda suka kasance duk mata ne,sai da ya rumtse ido sosai sannan yayi masaye wato ya canza su ya baiwa Agaishat ƴar wacan matar ita kuma ya bata ta Agaishat.

Cike da murna Alhaji ya ɗauki baby girl ɗin ya na mata huɗuba,tuni kuwa alhalin shi suka cika asibitin amman ƙememe ya hana kowa ya taɓa yarinyar.

A hankali Dr Ma'aruf ke shafa kan ƴar ƙanwar ta sa lokacin da Marâtre uwar marayun ta karɓe ta daga hannun shi "a kula da ita sosai ita ɗin marainiya ce mahaifiyata ta mutu wajen haihuwar ta sannan dama ta ce ko ta haife ta jefar da ita za tayi saboda ba ta hanyar aure aka haife ta ba"Dr Ma'aruf ke faɗar haka kafin ya tafi ya na jin son yarinyar cikin ɓargon zuciyar shi.

***

Cike da murna Rahama ta shirya saboda mafarkin da Mu'azam yace yayi,cikin ƴar ƙaramar motar shi suka shiga su dukan su har da Hajiya Babba ba su zarce ko ina ba sai gidan marayu.

Babu ɓata lokaci shugan gidan marayun ya kai su ɗakin da ake aje sabin haihuwa,marâtre ita ta rinƙa ɗauko jariran ta na miƙawa Mu'azam da ɗaya-ɗaya duk in an bashi sai ya aje.
"Inyaaa !inyaaa"haka jaririyar ke cancara kuka murmurshi dukansu ukun suka yi Mu'azam yace "alhamdullah na ɗauki wannan"marâtre tayi murmurshi tace "Allah sarki ko minti goma ba'a yi ba da wani likita ya kawo mana ita mahaifiyar yarinya rasuwa tayi"nan da suka cika takardu komi da komi Mu'azam yayi mata huɗuba ya juyo ya kalli Hajiya Babba yace "wane suna za'a saka mata?" "Fadimatu"ta bashi amsa ta na murmurshi shi ma murmurshin yayi yace "takwara kika yiwa kan ki kenan?to ni kuma zan rinƙa kiranta da *Mimi*".....

```JUMMA'A RANAR HUTUNA CE BAN POSTING```
[04/12 à 14:10] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Page 33-34*

Kiran Dr Ma'aruf marâtre tayi kamar yadda ya buƙata cewa duk ranar da aka samu wanda zai ɗaukar jaririyar ayi mashi magana.
Babu ɓata lokaci kuwa ya zo adresse ɗin Mu'azam ya karɓa sannan ya bi su har gidan su ya ga muhallin su kafin ya koma.
Wanka Hajiya Babba ta yiwa takwarar ta na ruwan zafi sai kuka ta ke canyarawa,mai ta shafa mata ta saka mata kaya masu kyau cikin wanda Mu'azam ya sawo mata.

Karɓar ta Rahama tayi ta shiga bata madara cikin biberon ai kuwa ta fara sha, Mu'azam ya shigo cike da murna yace "Hajiya Babba albishirin ki?"tace "goro"takardun gida ya ajiye a gabanta sannan ya zauna bisa tabarmar ya tanƙwashe ƙafafun shi yace "Dr nan ne ya bani kyautar gida mai kyau ɗan madaidaici sannan kuma har da kaya ya zuba cikin su,babban abun farin ciki da ya tambaye ni nayi karatu ko yaya ne nace mashi eh kawai sai ya bani shuwagabancin compagnie ɗin shi yanzu haka gobe zan fara aiki"wata irin buɗa Hajiya Babba tayi tace "madallah dama malam yace ita ɗin rahama ce gare mu ga shi kuwa tun ba'a yi nisa ba mun fara samun canjin ratuwa,kai masha Allah bari mu tashi mu fara shirin komawa can in ya so nan ɗin sai mu saka ƴan haya"ta na gama faɗar haka ta miƙe tare da shigewa ɗaki ta fara haɗa kayanta😹

Mu'azam ya kalli Rahama yace "ya na ga ba kya farin ciki?"murmurshin ƙarfin hali tayi dan ita sam ba ta so Hajiya Babba ta bi su can sabon gida🙄
Kwanci ta gyarawa Mimi sannan tace "ai abun murna ne sosai ga Ɗiyar nan sai kace kai ka haifeta dan har kama kuke yi"hannu ya sa ya ɗauki Mimi yace "kai haba bari na gani"Rahama tace "Allah kuwa kawai dai dan ta fi ka hasken fata ne"murmurshi yayi yace "farin mahaifiyarta ne tayi,kin ga an raba biyu ni na ɗau kama ke kuma kin ɗau farin fata"

Ranar nan su Mu'azam ba su kwana a ko ina ba sai a sabon gidan da Dr Ma'aruf ya basu wanda ke ADS can wajen masallacin jingile,Hajiya Babba sai zaga gida ta ke ta na kwararawa Dr Ma'aruf albarka.
```

***GIDAN ALHAJI

Cike da murnar yau Allah ya azurta shi da samun ƙaruwa ta Ƴa mace ya haɗa ƴar ƙaramar walima iya ahalin shi,zuwa yanzu duk yaran shi murna suke su ma sun samu little sis dama can su yawan aure-auren ne ba sa so.
Duk wanda ka gani fuskar shi a sake ta ke ya  mai nuni da farin ciki amman banda Ma'aruf da ya koma gefe ya na tunanin ya rayuwar ƙanwarsa za ta kasance duk da dai ya fara ingantata ta hanyar canza masu muhalli mai kyau.

Alhaji ya ɗauki baby girl ɗin sannan yayi gyaran murya yace "alhamdullah gida yayi ƙamshi,ya haskaka,ya girmama da zuwan Raihan"duk taɓi ɗiyan shi suka shiga yi Agaishat ta ɗan murmusa yayinda sauran matan Alhajin suka cicije.

Hidimar da ake ta shagaltar da mutane hakan yasa Hajiya ta zuba wani garin magani farin fal a cikin biberon 🍼 ɗin da ake baiwa Raihan ruwan zam-zam.
Cikin rashin sani kuma Agaishat ta ɗauka ta baiwa Raihan ruwan,ashe duk abinda ke faruwa a kan idon Ma'aruf

***

Mimi na cika kwana bakwai aka yanka mata ragon sunanta Fadimatu, gagarumin biki aka yi dan kuwa kusan dama Mu'azam mutumen jama'a ne.

Soyayya ƙauna suka haɗe gu ɗaya suka yiwa zuciyar Mu'azam ƙawanya sosai ya ke son Mimi fiye da komi na shi,a haka har Mimi ta fara girma ta fara ce mashi Daddy Rahama kuma Mami.

Mimi na cikin shekara ta biyu Allah ya yiwa Daddy wani irin buɗi na arziki,nan fah Mami ta aza masifa a doli suka tashi suka koma sabon gidan da ya gina yayinda Hajiya Babba kuma ta zauna wancan.

***Bayan 4years

Daddy ne da Mami zaune gaban Dr Ibrah wanda yanzu ya zama cikaken likita,bayani dai ya sake yi masu kan dukan su lafiyar su lau kawai su jira lokaci.
Su na shirin miƙewa yace "am tsaya na ɗibi jinin ku sai na kaiwa wani abokina mu ga shi mai result ɗin shi za ta bada"babu muso kuwa suka tsaya ya ɗiba sannan suka dawo gida.

Washegari tun da safe Daddy zai tafi aiki ya ja hannun Mimi suka fita tare ya biya ya aje ta gidan Hajiya Babba.
Fitar Daddy babu wuya Dr Ibrah ya shigo gidan,sai da ya shigo falon ya ƙwala sallame.Mami ta fito daga ita sai kayan barci jigida nayi mata kacau-kacau cak ta tsaya ganin ashe ba Daddy ba ne,har za ta juya sai taji muryar Dr Ibrah "masha Allah a nan Allah yayi babba ƙaddara wacce ba ta dace da baƙar fata ba"da sauri ta juyo ta na kallon shi .

Gira ya ɗaga ya ajiye takardun hannun shi ya fara takawa zuwa gare ta,wuyanta ya sunsuna yace "Hummm komi ma na Gimbiya haɗaɗe ne"lumshe ido Mami tayi ta na jin tsikar jikinta na tashi.

Wuyanta Dr Ibrah ya fara yiwa kissing kafin ya koma ga lips ɗin ta,cikin ƙanƙanan lokaci ya birkita mata lissafi.Ɗaukarta yayi cak ya nufi ɗaki da ita,abinda Mami ba ta taɓa tunani ba shine ya faru wai ita ce tayi zina da wayon ta.
Kuka ta shiga yi sosai Dr Ibrah na bata haƙuri,ganin ta ƙi barin kukan yasa ya kimtsa ya bar mata gidan kafin a rutsa shi.

Da marice Daddy ya shigo gidan amman sai yaji shi tsit, ɓangaren Mami ya nufa yaji ƙofar a ƙage fitowa yayi ya nufi kitchen dan ya ga babu komi a dining nan ma wayam .
Falo ya dawo ya zauna idon shi ya sauka da farar takarda,ya ɗauka ya karanta sai ya miƙe murmurshi kan fuskar shi ya nufi ɗakin shi wanka yayi sannan ya kira Dr Ibrah amman har ta gama ringing bai ɗauka ba.

Motsin da ya ji yasa shi waiwayo Mami ce kallonta ya tsaya yi ganin tayi wani irin sanyi"ashe har ka shigo ?barka da zuwa ina Mimi"
"Yauwa!ta na gun Hajiya Babba yau amarci ni ke son mu sha sosai"ya ɗaga mata gira gabanta ne ya faɗi sai ta ke ganin tamkar zai gane ne in ya kusanceta.

"Ayya Daddyn Mimi banda lafiya kuma"da sauri ya kai hannun shi kan wuyanta ai kuwa yaji kamar da alamar zazzaɓi,magani ya bata sannan ya fita ya nemo masu abinda za su ci su da masu gadi.

Sai da aka kwashe wata ɗaya cur sannan Mami ta fara sakin jikinta ta koma kamar da,Mimi kuwa na gidan Hajiya Babba zamanin ta.
Tun da safiya ta waye ta ke zabga amai,babu ɓata lokaci Daddy ya kaita asibiti awon farko Dr Ibrah yace mashi "congratulations kai ma ka kusa zama baba"da murna Daddy ya rungume shi can kuma ya sake shi yayi sujada shukur.

Gira Dr Ibrah ya ɗagawa Mami ya mata nuni da cikin jikinta sannan ya nuna kan shi ma'ana dai ciki na shi ne ba na Daddy ba,kawar da kai tayi gefe dan dama tun farko ba tayi wata murna ba.
Murmushi ta saki tare da ambaliya hawayen baƙin ciki na da aurenta za ta haifi shege a zuci tace "lalle na tabbata *KARUWAR GIDA* tunda har zan haifi ɗan da ba na mijina ba"Daddy kuwa a tunanin shi kukan murna Mami ta ke a haka ya kwasheta suka wuce gidan Hajiya Babba.....
[05/12 à 14:08] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Page 35-36*

Haka Mami tayi rainon cikinta har ta haifi ƴarta mace aka saka mata suna Ameera,sosai Daddy ke nunawa ƴaƴan nashi so amman ya fi ƙaunar Mimi.
Sam ba za ka ce Mimi ba ƴar su ba ce yadda suke ririta ta da nuna kulawar su fiye da Ameera,lokaci zuwa lokaci Dr Ibrah ya na kawowa Mami farmaki a duk lokacin da Daddy ya fita tun ta na kaucewa har suka ɗinke kullum sai sun yi RDV.

Ameera na da 3years Mami ta kuma samun wani cikin,sosai Daddy ya nuna murnar shi.Ita kuwa Mami masifa ta rinƙa yiwa Dr Ibrah na ya munafinceta bai yi mata allura hana haihuwa ba,to daga nan ne suka yi baran-baran suka rabu Mami ta tuba.
Cikinta na shiga watan haihuwa ta haifo Twins duk mata aka sa masu Imane da Ihsane to tun shi ba ta sake haihuwa ba.

***Cigaban labari

Wani irin gumi ne ya shiga ketowa Daddy,sam bai tsammaci haka ba tunanin shi ma bai taɓa kawowa da rainon ƴaƴan wani ya ke ba.

Ana cikin haka wayar shi ta ɗauki ringing *Dr Ma'aruf* ya gani cike da mamakin kiran Daddy ya ke kallon screen ɗin wayar dan an fi shekarar da tafi goma rabon shi da Dr Ma'aruf ɗin,zai iya cewa ma tun tashin su daga gidan da ya basu saboda ya sha gwada lambar amman ba ta shiga.

Sai da ta tsinke Daddy bai ɗaga ba,wani kiran ya shigo danne zuciya yayi ya ɗaga kiran ba tare da yace komi ba "Assalamu alaikum Alhaji na zo gida ne sai na gan shi a rufe"
"Ina Clinic Agaji ne Madam babu lafiya"ba'a ƙara cewa komi ba daga ɗayan ɓangaren aka kashe wayar.

Can kamar minti ashirin sai ga wata dalleliyar mota tayi parking a harabar asibitin,su uku ne duk sukafito Alhaji ne,sai Agaishat da kuma Ma'aruf wanda shi ya tuƙo motar.

Dialing number Daddy yayi ya na ɗagawa yace "am ka fito mu na harabar asibitin"da "toh"Daddy ya amsa ya miƙe a kasalance ya fito.
Gaban shi ne ya faɗi lokacin da yayi tozali da Agaishat wacce ta ƙurawa hanya ido,ƙarasowa yayi amman ya kasa ɗauke idon shi kanta saboda tsantsar kama da Mimin shi da ya ga ta na yi.
Hannu ya basu suka yi musabaha yayinda suka fara tambayar shi mai jiki,jin murya Agaishat kuma ya sa zuciyar shi yin rauni tabbas ko makawo ya laluba ya san wannan jinin Mimi ce.

Murmushi Dr Ma'aruf yayi haɗi da sosa ƙeya yace "in ba za ka damu ba ina son mu ɗan zauna za mu yi magana"ya faɗa ya na mai ɗan waige-waige.

Murmushi Daddy yayi yace "maganar mi kuma Dr ?bayan tun kafin ka faɗa na san kun zo nan ne dan ku raba ni da Mimina"ya yi maganar cikin tausayi yayinda idon shi da suka yi ja tun ɗazu suka cika da ƙwalla.

Alhaji yace "Ma'aruf kenan dai dagaske ɗin ne Allahu Akbar"ya faɗa ya na mai zubewa ƙasa ya na sujidah  shukur kafin ya ɗago ya fashe da kuka kuma😹 Agaishat ma kukan ta taya shi.

Waje suka samu can ƙarƙashin innuwar mangwaro suka zauna Dr Ma'aruf ya shiga baiwa Daddy labarin komi dangane da haihuwar ƴaƴa Mazan da Allah ke azurta Abban shi sai Mimi ce kaɗai mace.

Ajiyar zuciya Daddy ya sauke yace "to miyasa ba ka barta cikin gantan ta ba?"Dr Ma'aruf yace

"saboda kar a cutar da ita,na san in na barta za'a kasheta ne saboda su sauran matan ba sa so ace an fifita ƴar kishiyar su fiye da nasu ƴaƴan kuma maganar da ni ke yi maka yarinyar da na masayan tuni suka kasheta duk da ƙoƙarin kariyar da nayi ta bata"

Cikin son kawar da zancen tashin hankali nan Daddy yace "yanzu dai Mimi ta na Niamey in shaa Allah gobe zan sa su dawo"

Mimiƙewa suka yi sun so shiga duba Mami amman Daddy ya hana ta hanyar ce masu barci ta ke,su na tafiya Daddy ya kira Alhaji Kamal yace ya yiwa su Hajiya Babba réservation ta dawowa gobe ya na gama faɗa ya kashe wayar shi kwata-kwata.
Takarda ya samu gun Dr ya yi rubutu ya aje ta kusan kan Mami kafin ya fice,bai zarce ko ina ba sai gidan Hajiya Babba .
Toilet ya shige ya sakarwa kan shi shower,a sannu ruwan ke dukan fatar jikin shi lumshe ido yayi ya na tunanin rayuwa hawaye idon shi suka shiga fitarwa.

***

Arerewa haɗi da shewa Lami tayi tace "wuuu *KARUWAR GIDA* an kusa saukewa,a toh dama ƴan jami'a ai duk ƴan iska sun fi yawa yanzu ba sai ayi mu gani ba in tusa ta hura wuta sai mu ga yadda za'a yi karatun hhh"ta ɓaɓake da wata dariya mugunta.

Shiru Anna tayi ta na nazartar kalaman Lami kafin ta maido duban ta ga Fadila wacce tayi fari fyarau ta ƙara ƙiba,kallon da Anna ke yi mata ne yasa ta tsargu kawai sai ta miƙe ta nufi ɗaki.

Tafiyarta Anna ta bi da kallo ta na sake tantance ta,ko minti ɗaya Fadila ba ta yi ba Anna ta shigo.Da sauri ta juyo ta na kallon mahaifiyarta ta haɗi da zare ido kamar wacce ta yiwa sarki ƙarya.
"Cire min hijabin jikin ki baƙar munafuka"cewar Anna ta na harar Fadila,kasa cire hijab ɗin tayi hakan yasa Anna ta ja hijabin da ƙarfi ta cire.
Taɓa hannuwa ta shiga yi ta na salalami sakamakon cikin Fadila da ta gani kamar ƴar ƙwarya ya fito yayi mata wani cercle ai Anna ba ta san lokacin da ta ɗauke ta da mari ba ta shiga dukanta haɗi da tambayarta uban wa yayi mata ciki amman ta ƙi faɗa.

Sai da taji wuya sosai sannan tace "Nasir ne Anna"wata uwar gwabza ta kaiwa bakinta nan take jini ya ɓalle,ƙetare ta Anna tayi ta shiga ɗakinta ta ɗauki hijabi ba ta zarce ko ina ba sai gidan su Nasir .

"Uban da ya ɗaura auren uwarka da uban ka Allah ɗebe masu albarka,asarare haihuwar asara da yarda Allah ba za ka gama da duniya lafiya ba"wannan shine abinda Anna ta faɗa lokacin da ta shigo gidan su Nasir madadin sallama.

Duk fitowa suka yi suna kallon ikon Allah, Iyani ta fito daga banɗaki kallon kwabo saura takwas ta yiwa Anna kafin tace "baiwar Allah daga gidan mahaukata kika gudo da za ki shigo mana gida ki na zage-zage?"

"Kutumar uban can!ba ki ma gane ni ba?to uwar Fadila ce wanda tanbaɗaɗen yaron ki ya ɗirkawa ciki"dariya Iyani ta fashe da shi tace "to sai mi dan yayi mata cikin?ai haka duniya ta ke dama abinda aka yiwa naka wata rana na ka ɗin ne zai yi ma wata dubi can ƴata ce nima wanin ne ya mayar da ita haka"ta ida maganar ta na mai nuna mata Fauziya wacce ke tsaye da ƙaton cikinta duk ya mayar da ita wata kala.

"Ina ruwana da ƴar ki ni tawa na sani dan haka ki shaida mashi da zarar ya dawo,gobe kotu za ta raba mu"ta na gama faɗa ta fice,tsuki Nabee tayi ta koma ɗaki a zuciyarta ta na mamakin yadda har ƴan mata suke sakacin baiwa namiji kansu kamar shashashu koko dan ba su ƙwarai a barikin ba ne ?oho

***

Cike da masifa Hajiya Babba ta shiga balbale Alhaji Kamal da faɗa sai kace ba sirikin ta ba,a haka dai ta tattare kayan su ni kuwa sai murna ni ke zan koma gida gun Daddy.

Washegari 16h tuni motar mu ta dira a Maradi, drever Daddy ya aiko ya ɗauke mu.
Gidan Hajiya Babba aka kai mu,da murnata na buɗe mota na fito na shiga da gudu ina "Daddynaaa "cak na tsaya gani baƙin fuska duk miƙewa suka yi suna kallona nima haka sai dai na tsayar da dubana ne ga mai irin fuskata.

Murmushin da yafi kuka ciwo Daddy yayi yace "Mimina "a Shagwaɓe na je na faɗa jikinsa ina turo baki nace "i miss You Daddyna shine ka ƙi tafiya ka tarbo ni ai da kai na so idona su fara gani sai kawai ka turo min drever"laƙace min hanci yayi yace "ba ki ga baƙi ba ne?"juyawa nayi gun su sai na ga ashe mu su ke kallo.

"Yau na ga ragguwa yarinya dan rashin tausayi kika bar ni da dakon ƙaton aljanin ki,ina dalili

yarinya kamar wata..."maganar ce ta maƙalewa Hajiya Babba ganin ashe da mutane falon gaisheta suka shiga yi ta na amsawa tare da yi masu kallon ko ina ta san su.

Teddyna ta jefo min ta na hararena nayi dariya ina kakaɓe shi dan ya faɗi, Hajiya Babba na zaunawa Daddy yayi gyaran murya ya fara bada labari tiryan-tiryan tun daga ranar da aka ɗauko ni daga gidan marayu.

Hawaye shararaaa haka suke zuba a idona na ƙurawa Daddy su ƙyaftawa ban yi,hutu na wucen gadi kwanyata ta tafi ba ta dawo ba sai da naji Daddy na cewa "Mimi ga biologique parents ɗin ki nan".....
[07/12 à 07:45] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Page 37-38*

Banda kallo babu abinda nayi saboda sam zuciyata ta kasa yin aikinta daidai ya da ya kamata, Agaishat ta taso daga inda ta ke ta zo ta rungume ni wani yammm naji da sauri na sauke ajiyar zuciya ita kuwa kuka ta ke.
Samun bakina nayi da furta "Momyyy"cire ni tayi daga jikinta ta ƙurawa fuskata ido ta na murmurshi tace "dauther ina son ki sosai na godewa Allah da gwada min wannan rana,ta so ki je gun Abban ki saura kaɗan zuciyarsa ta buga saboda ke"ta faɗi haka ta na mai miƙar da ni tsaye mu ka nufi gun dattijon arziki wanda ya ƙura min ido tun shigowa ta.

Duƙawa nayi zan gaishe da sauri ya jawo ni na faɗa jikinsa,wasu sanyayun hawaye suka shiga malala a idon shi "Fadimatu na? Allah raya ki a kan sunnah ya tsare min ke daga sharrin ƴan hassada da baƙin ciki..."kuka ne yaci ƙarfinsa sai ya ƙyale.

Hajiya Babba wacce tayi suman zaune tace "oh Allah duniya babu kyau an raba tsoka da jini gudun mugayen ɓoye,ina ta Rahamun ta ke ta san da maganar ?baiwar Allah ta so Mimi kamar ranta"ɗagowa Daddy yayi da jajayen idonsa yace "na saketa ai"da sauri duk mu ka kalle shi dafe zuciyar shi yayi sannan yace "laifi ta yi min mafi muni wanda duk mai ƙaunata ba zai bari na cigaba da zama da ita ba,Rahama ta cuce ni Hajir mu ta rasa da wanda za ta ci amanata sai da babban abokina"

"Mine?cin amana kuma?"cewar Hajiya Babba shiru Daddy yayi dan sai yanzu ya gane da bai kamata ya faɗi haka ba "Mimi tashi kije ki yi wanka"cewar Hajiya Babba ,jiki ba ƙwari na miƙe

tare da nufar part ɗin ta.

Sai bayan Mimi ta tafi ne sannan Daddy ya fayyace masu komi Hajiya Babba kuka ta saka Momy na bata haƙuri,Abba kuwa nasiha ya shiga yiwa Daddy dan ya ɗauke shi tamkar ɗan cikinsa.
Dr Ma'aruf ya gyara zama yace "gobe ka same ni a asibitin mu zan duba na hauda ka kan magani, sannan ka kawo min result ɗin da sauran suka yi ma gwaji" Daddy yace "in shaa Allah na gode".

Dakyar suka daidaita nutsuwar su suka fara shan fruits,ni kuwa ko da na gama wanka na shafa mai da turare kayan da Hajiya Babba ke tara min na ciro riga t-shirt fara da buje blue na jeans. Tunda na fito mu ka haɗa ido da Daddy wanda ke saiti da ƙofar ɗakin, murmurshi na sakar mashi shi kuwa Daddy zuciyarsa ce ta shiga bugawa ganin na shanun Mimi sun yi tsiriri a tsaye suna zagin sa😹kawai haka yaji haushi ko bra ba ta saka ba za ta fito haka alhalin akwai mutane falon.

A shagwaɓe na faɗa jikin Daddy daga zuwana "shine ka fara ci ka manta da ni"na faɗi haka ina mai amshe apple🍏 ɗin hannunsa, murmurshi yayi yace "Mimi uwar rigima ai na zata ma kin kwanta saboda gajiya,yanzu yaya kike ji komi normal ?"Kai na gyaɗa na guntsiri apple ɗin daidai shatin haƙoran sa sannan nace "Daddy wai sai yaushe Tantie Munawara za ta sauka daga dokin kafiya? ni dai na matsu na gan ta mijinta na da kirki"Daddy yace "sai ranar da kasuwar apple ta tashi"ya faɗi haka ya na kimtse dariya,ƙafafu na shiga bugawa ina kukan shagwaɓa nace "Allah ba santi nayi ba kawai dai na tambaya"

"To Sarkin surutu sai ki sauko ki ci abinci dan na san in an biye ta taki ba za ki ci ba"cewar Hajiya Babba ta na juye dafafun zabi wanda suka sha jar miya kallon Daddy nayi nace "ni ba zan ci ba kar na ɓata hannu na"murmurshi yayi dan ya san mi ni ke nufi a duk lokacin da nayi sha'awar ya ciyar da ni da hannunsa haka ni ke faɗa.

Hajiya Babba ta taɓe baki tace "na ga yaushe za ka barin sangarta ƙatuwa har haka wai fah sai dai ya bata a baki kamar jaririya "cikin shagwaɓar da ta zame min jiki nace "ni dai ba ƙatuwa ba wai duka-duka ma nawa ni ke da ake sa min ido?haka fah jiya ta ƙi ban abinci a baki alhalin Daddy cewa kayi ta je ta kula da ni"duk dariya aka yi Hajiya Babba tace "ah to ni ban iya gantali ba ƙatuwar budurwar da ko yau sai a ɗaura mata aure zan baiwa abinci a baki dan dai duniya ta zo ƙarshe can shi da ya sangartar da ke ya baki"

Baki na turo nace "to na ma fasa ci ban so"na faɗa ina shirin tashi Daddy ya mayar da ni na zauna "miye haka Mimi ki nutsu mana ko ba ki ganin ba mu ɗaya ba ne akwai baƙi?koko so kike

Abba yace na sangartar mashi da yarinya?"Daddy ya raɗa min a kunne,turo baki gaba nayi na juyo ina facing shi har zan yi magana ya aza min yatsansa a baki.

Cikin plate Hajiya Babba ta zuba min Daddy ya karɓa ya na bani shi ma ya na ci,yayinda su kuma suka gewaya suna ci su ma.
Ƙurawa Daddy ido nayi ina jin wata irin ƙaunarsa a raina,shi ma jefi-jefi ya ke kallon ƙwayar idona.Sai da mu ka ci mu ka ƙoshi sannan Daddy ya aje plate ya zuba mana jus,miƙewa nayi na fita zuwa harabar gidan.
Iskar Ubangiji na shaƙa na lumshe ido,an ɗauki kamar minti goma suka fito Hajiya Babba riƙe da hijabi a hannunta saka min tayi kafin na tambayeta lafiya naji Daddy na cewa "Mimi sai in na zo ki kula da kan ki"idona ne suka yi rau-rau na kalli Daddy nace "zuwa ina?"Hajiya Babba tace "ai kaji sakalci Abban ki za ki bi kuje can gida"wani kukan kura nayi na faɗa jikin Daddy na ririƙe shi ina kuka tare da girgiza kai.

Rumtse ido yayi ya na jin abubuwa na mashi yawo a kwanya,na ɗaya saukar dukiyar Fulaninta a kan ƙirjinsa na biyu sautin kukanta.Dakyal ya aro jarumta ya shiga bubuga bayanta,cikin murya mai taushi gami da kasala yace "yi shiru Mimina ai zan zo zuwa dare "kafaɗa na maƙe ina gyara kwanciya kan ƙirjinsa.

"Ku shiga mota ina zuwa"cewar Daddy,wucewa suka yi Hajiya Babba kuma ta koma ciki saboda karyewa da zuciyarta tayi.
Haɓata ya ɗago ya ƙura min ido,ta saman gashin idona da suka jiƙe da hawaye ni ke kallon shi.Iska ya fara hura min a fuska na lumshe ido ina sauke ajiyar zuciya, daidai saitin laɓana naji ya sauke na shi kafin ya janye yace "ina son ki,ki kula da kan ki ke ɗaya ce mace a can ƴan uwan ki na can na jiran ki saboda bege"idona na a lumshe nace "Daddy mu je tare"murmurshi yayi mai ɗan sauti ya cire ni daga jikinsa ya ja hannu na zuwa mota ina hawaye ina ji ina gani Daddy ya buɗe seat ɗin baya ya sanya ni ya rufe.Wani kukan ne ya kubce min ina leƙen Daddy ta glass Ma'aruf ya yi mata key mai gadi ya buɗe mana gate.

**Cike da tashin hankali Mami ke duba takardar,ihu tayi ta dire daga bisa gado ta fito daga cikin asibitin.Direct bakin hanya ta nufa ta tari mai adaidaita,ya na sauketa ta shiga ciki a falo ta tarar da Ameera ita da Twins duk sun dawo daga school.
Ɗakinta ta shiga ta ɗauko kuɗi ta miƙawa Ameera ba tare da tace komi ba ta nuna mata hanyar waje hakan yasa Ameera fita,Twins kuwa sai sannu da dawowa suke yi mata amman ta ƙi kula su.
Dr Ibrah ta kira ta shaida masa komi dariya ya shiga ƙyarƙyatawa kafin ya kashe kiran,ba'a fi

minti goma ba ya zo gidan.Da gudu Twins suka rungume shi suna mashi oyoyo,Ameera kuwa yi tayi kamar ba ta san da zuwan shi ba.
Mami ta fito ta na kuka,Dr Ibrah ya taɓe baki yace "to miye na kuka dan ya sake ki?kuma fah yaran nan duk kin san ni ne mahaifin su to damuwar ta mi ce?"kai Mami ta girgiza tace "na cutar da Mu'azam na haifa masa shegu cikin gida ya ciyar da su haɗi da ɗawainiya yanzu kuma har gidan ya ce ya bar min ba zai iya sake rayuwa cikin sa ba"ta ida maganar cikin fashewa da kuka.
Ameera ta miƙe tsaye ta na jin abun kamar almara "ni ne sabon Daddyn ku kun ji ko?daga yau Daddy za ku kira ni kun ji ko?"Dr Ibrah ya faɗa ya na rungume Twins .
Kuka Ameera ta fashe da shi ta fita da gudu da sauri Dr Ibrah ya fito ya na kiran sunanta ganin haka yasa mai gadi liƙe ƙofa.
Ƙarasawa Dr Ibrah yayi ya ɗauketa da wani gigitacen mari yace "gidan uban wa za ki je?"cikin kuka da rashin tsoro tace "gidan uban ka zan je shege zakka ɗan asara da ba zai ganin Annabi ba da yarda Allah mutuwa kare za ka..."waro ido yayi ya sake ɗauke ta da mari kafin ya fincikota ya shiga bal da ita a ƙarshe ya jata ƙiii zuwa ɗaki.
Banda kuka babu abinda Mami ke yi tare da dana sani maras amfani,ganin bugun da Dr Ibrah ke yiwa ƴarta yasa ta miƙe da sauri Ameera tace "kar ki taɓa ni ban son ki ban ƙaunar duk mai ƙaunar ki sannan sai na shiga duniya na zama shaƙiƙiyar tantiriya sai na kawo maki shegu kin raina tunda rainon su kawai kika iya"tayi maganar ta bubuga hannunta da table.
Cak Mami ta tsaya ta na jin zuciyar ta na barazanar faɗowa,tabbas ta san Ameera ta aika yin karuwanci ga ɗiyar *KARUWAR GIDA* ai ƙaramin abu ne amman sam ba za ta lamunta ba.

***GIDAN ALHAJI

Tamkar wata tv haka duk suka sani a gaba su na kallo duk yaran murmurshi kan fuskarsu yayinda matan suka turniƙe fuska kamar tsohon kashi.
Momy kuwa ta na zaune kusa da ni ta riƙe hannuna gam,Abba na zaune daga gefe ya na murmurshi Dr Ma'aruf yace "tanti amaya ya kamata a kai little ɗaki ta huta kin sa da gajiya a jikinta"murmurshi Momy tayi ta ja hannuna zuwa ɗakinta.Lafiyayen gadonta ta nuna min na kwanta bisan shi, hasken ɗakin ta kashe min na rungume pilow ina jin wasu hawaye na ziraro min kewar Daddyna ni ke yi murmushi nayi tuna ba shine biologique parent ɗina ba.....
[08/12 à 16:05] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Page 39-40*

Kamar yadda Daddy yayi alƙawali da dadare sai gashi kuwa,kowa na gidan ya hallara banda Mimi wacce rashin sabo ya sa tayi zamanninta a ɗaki.

```gani a cikin gidan ku amman ban gan ki ba``` shine text ɗin da na karanta wanda ya fito kuma daga Daddyna,zumbur na miƙe ko kallabi ban saka ba balle wani hijab da ɗan guduna haɗi da murna na nufe shi na faɗa jikinsa duk da kuwa ƙoƙarin hana ni da ya so yi.

"Daddy ka zo ka tafi da ni ne?dama ni na gaji ni ɗaya babu su Twins kuma Teddyna ya na can gun Hajiya Babba"na faɗa ina mai kwantar da kaina bisa kafaɗarsa,sumar kaina ya shafa yace "Mimi ai kin zo gida kuma ke da can sai in kin zo ganin mu"da sauri na girgiza kai nace "a'a Daddy dan Allah kar ka bar ni nan wlh ban san kowa ba kuma fah su nan babu mace ƴar yarinya to da wa zan yi hira?"dariya kusan rabin mutanen suka yi kafin Dr Ma'aruf yace "ai shiyasa Abba ke son ki dawo nan ɗin amman kar ki damu zan cewa Fatima (cewa da Ɗiyar shi)ta dawo nan da zama"kafaɗa na maƙe na jimƙe hannun Daddy.

Mutanen falon duk Alhaji ya sallama ya bar Momy da Ma'aruf kawai wanda tun ɗazu suka yanke shawara duk da ba su san ko Mu'azam zai karɓeta ba ni kuwa ina jikin Daddy na lafe kamar mage.
Gyaran murya Abba yayi yace "Mu'azam banda bakin gode maka sai dai in ce Allah saka maka da alkhairi ya biya maka buƙatunka duniya da lahira,sannan a ƙarshe ina neman wata alfarma dan Allah amman sai ka min alƙawari za ka amince"ɗagowa Daddy yayi kalli Abba murmurshi kan fuskar shi yace "to Abba ina jin ka in shaa Allah "

Sai da Abba ya sake nutsuwa sannan yace "ina son ka cigaba da riƙe min Fadimatu a gun ka na san za ka fi kula da ita sai dai wannan karon ba'a matsayin Ƴa za ka riƙe ta ba a matsayin mata"da sauri Daddy ya zabura yace "Mata?mata dai?aure? Mimi? Abba..."hannu Abba ya ɗaga yace "kar ka manta ka min alƙawali"Daddy yace "ita fah Mimi yarinya ce har yanzu kuma kamar an cuce ta an gama ta da tsoho"dariya Ma'aruf yayi yace "haba Mu'azam duka-duka nawa kake ba fa za ka wuce 45years ba amman bari mu tambayi Mimin Daddy ko ta amince"ya ida maganar cikin barkwanci.

Ƙara ɓoye fuskata nayi cikin ƙirjin Daddy dan duk abinda su ke ina jin su magana ce kawai ban yi,yadda Daddy ke shafa gashin kaina yasa barci ɗauke ni ban ma san abinda suka yanke ba akai.

Washegari da asubah Momy ta tashe ni nayi sallah,ina gamawa na zumɓuro baki ganin ashe wayo Daddy ya yi min bai tafi da ni ba.
```

Momy da ke daga gefe ta na lura da Mimi kai kawai ta girgiza ta na jin son ƴarta har ƙasanƙasan zuciyarta,zuma ta miƙo min wacce ta sha haɗi ni kuwa Uwar son zaƙi na shiga sha. Wayata na ɗauka na danna kiran Daddy sai turo baki ni ke yi ina tsara yadda zance mashi amman har ta gama ruri bai ɗauka ba.
Daddy kuwa da ke can kwance cikin ɗakin shi tun na farko kafin su tashi daga gidan Hajiya Babba kwanci ya gyara ya na mai cigaba da kallon hotunan Mimi,sam ya kasa daina kallon ƙirjinta tunda aka bashi ita aurenta ya samu kan shi da kalle surar jikinta.

Kiran ya maida mata,ni kuwa ganin appel ɗin shi yasa na ɗauka cikin sanyin murya nace "Daddyna ina kwana?shine jiya ka tafi ka bar ni a nan haba dai"na ida maganar cikin shagwaɓa.

Numfashi ya fesar kafin yace "Mimina?"a yadda yayi maganar yasa ni yin shiru ina jin zuciyata na bugawa "Mimina?"ya sake faɗa "uhum!"murmurshi yayi mai sauti yace "rigima ko?"ido na rufe na turo baki gaba nace "ba kai ne ka bar ni ba"Daddy yace "yaushe kike son dawowa nan ɗin ?"cikin zaƙuwa nace "yau ni ko yanzu ma"Daddy yace "kenan na faɗawa Abba a ɗaura auren yau?"kai na girgiza kamar ya na gani na dan wani tsoro ne ya zo shige ni nan take.

"Kin yi shiru ko ba ki shirya zuwa gidan ba?"ya tambaye ni,a sanyaye nace "na shirya mana amman gun Hajiya Babba zan zauna"dariya Daddy yayi yace "naji kar a kawo ki guna kenan?"da sauri nace "eh" "tsorona kike Mimi?"yayi tambayar cikin kalar tausayi nace "a'a Daddyna"ya sauke ajiyar zuciya yace "kin ci abinci ne ?"na bashi amsa da "a'a Momy dai ta bani zuma ga kuma madara ta kawo min jira ni ke ta wuce in sha"shiru Daddy yayi ya na jin tausayinta a ran shi dan kuwa tuni ya gane an fara gyaran amarya ne.

"Ok to ɗauki ki sha da zafin ta sannan in kin yi wanka ki saka kayan da na kawo maki jiya Please kar kice ba za ki saka bra ɗin ba"Daddy ya faɗa ya na yanke kiran.
Ajiyar zuciya na sauke na ɗauki madarar da Momy ta aje na fara sha ina yamutsa fuska saboda goût ɗin hulba da naji.

***Bayan 1week

Tuni aka kawo lefena akwatina dozin kowane cike da kaya,tuni kuma Momy ke ta min gyaran jiki da na km.Cikin ƙanƙanan lokaci na canja na ciko sai sheƙi ni ke yayinda kuma ko muryar Daddy naji sai na wanke pant😹 ban san dalili ba,sosai mu ka shaƙu da Daddy na ɓangaren soyayya sam bai nuna wata kunya dan zai aure ni balle ni da dama na mutu cikin ƙaunarsa da

son shi.
In muna waya da Daddy za ka ɗauka da wani ƙaramin yaro ne ɗan 27years yadda ya ke tsayawa ya saurare ni ya biye min wajen shirme da sangarta hadi da shagwaɓa.

A yanzu na saba da gidan mu ga kuma Fatima da ta dawo gidan mu wacce kusan sa'ata ce sai dai na girme ta,duk da ta na zaman ɗiyata amman ni a abokiya na ɗauketa.Ita ke min rakiya in zan je wani gun sai Daddy ya zo ya kai mu in mun gama abinda muke ya je ya ɗauko mu.

Abu guda ne ya tsaya min a rai yadda kwata-kwata Daddy bai son nayi mashi maganar Ameera balle uwa uba Mami,yanzu ma mu na zaune a mota mu na hira bayan ya maido ni daga gyaran gashi.
Wayar shi na karɓa ina kallon hotuna cikin gallerie yayinda shi kuma ya ke kallona lokaci zuwa lokaci ya na sauke ajiyar zuciya wacce tuni na gane ta bege na ce dan ni ba yarinya ba ce na san da Daddy ya na fama da sha'awa haƙuri kawai ya ke yi.

Hoton wata mage na gani na ɗago ina cewa "ina son irin wannan magen Daddy please ka sa a nemo min"laɓana ya tsurawa ido,babu zato babu tsammani naji saukar bakin shi kan lips ɗina da sauri na rumtse ido ina jin zuciyata na bugawa yayinda jikina ya ɗauki kyarma.

An ɗauki tsawon min biyar kafin ya janye daga jikina,sunkuyar da kai nayi ina jin wata kunya. Kan shi ya ɗora saman volant ya rumtse ido ya na sauke ajiyar zuciya "bani gorar ruwa "ya faɗa cikin kasala duƙawa nayi kusan ƙafafuna na zaro ɗaya na miƙa mashi ya ɓalle murfin ya fara shan ruwan.

"Mimi dan Allah ki fara shirin tarbata tun ranar farko kin dai ga halin da ni ke ciki"Daddy ya faɗa ya na mai jingina da kujerar mota, rau-rau idona ya kawo ruwa dan tsoro da jajayen idon shi ya tsare ni.....
[10/12 à 16:05] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Page 41-42*

"Ni dai a'a sai na gama karatu"na faɗa ina matsar ƙwalla,shiru Daddy yayi ya na kallona can ya

nisa yace "sam hakan ba zai yiyu ba Mimi kuma maganar karatu ki mayar da shi gefe sai wata shekara kuma,yanzu time ɗin kula da ni ne"ɗagowa nayi ina kallon shi jin abinda ya ke faɗa kai na girgiza nace "please Daddy"kawar da kai yayi gefe dan kuwa sam bai ji zai iya cutar da kan shi ba alhalin Mimi ta isa ɗaukar nauyin namiji.

Jiki na min rawa na kamo tafin hannun shi wanda ya ke masifar sanyi ba kamar nawa ba da ya ke rau da zafi,dan kuwa kullumin jikina cikin ɗumi ya ke.
"Daddyna please ko yi za kayi ka bari har mu saba"cike da mamaki ya juyo yace "Mimi wane sabo kuma bayan wanda mu ka yi?"na turo baki nace "ni dai ban saba da kai ba"lips ɗin ta ya ƙurawa ido kafin kuma ya kawar da kai gefe dan ya na tabbacin in ya cigaba da kallonta to tabbas sai ya sake kai bakin shi ga laɓanta.

"Ki shiga ciki Mimi in na isa gida zan kira ki"Daddy ya faɗa ya na kunna mota,cikin ƙin jin daɗin rabuwar da za mu yi na fita bayan nayi mashi kiss ga kumatu.
Wajen da sanyin laɓanta ya sauka ya shafa ya na murmurshi kafin ya fara tuƙa motar mai gadi ya buɗe mashi gate.

***

"Wayyo Allah Anna zan mutu,wai wai Allah Innalillahi Allah na tuba ka yafe min wayyo na shiga uku na lalace"Fadila ke faɗa ta durƙushe tsakar ɗaki farin ruwa gami da jini na zuba ta ƙasanta yayinda Anna ke gefe ta na kallonta sai da kan ɗa ya sawo kai sannan Anna ta matso ta fara taimaka mata.
"Inyaaa"jariri ya canyara kuka yayin shaƙar iskan duniya,reza ta sa ta yanke cibi kafin ta aje babyn gefe ta kimtsa Fadila wacce ke fitar da gumin wahala.

Duk muƙu-muƙun Anna na kar ƴan unguwa su san da Fadila na da ciki ya tashi a banza,domin kuwa Lami ta fita ta gayyato matan unguwa suka kusa cika gidan a kunnen su kukan farko na yaro ya sauka ai suka shiga taɓa hannuwa kowa na faɗin albarkacin bakin sa.

A harzuƙe Anna ta fito ta na masifa ta na cewa "to ƴan gulma miye sabo a duniya?ina ce dai ba gare ta farau ba balle ya ƙare kanta kuma mutum bai san mi zai faru gobe ba sannan mai baya dayawa(zuri'a)bai faɗin aibun Ɗan wani"ai fah kuwa da sannu suka fara sulalewa.

A ɓangaren Nabee kuwa duniyar ta bisa tsinke ta ke ci musamman da ta samu wani Alhaji

Waleed,duk da dai ya na da halin banza na bin mata amman shi tsakani da Allah ya ke son Nabee.
Cikin sigar roƙo yace "my Nabee kiyi haƙuri na turo manya su sa baki ayi auren nan da wuri wlh a matuƙar matse na ke na gan ki a gidana"kallon ƙaton tumbinsa Nabee tayi sannan ta ƙirƙiro murmushin ƙarya tace "haba dai duka-duka nawa na ke da zan yi aure yanzu?a'a ka bari duk ranar da na shirya ni zan faɗa ma lokacin da za ka turo kayan auren "ta ida maganar ta na sunne kai wai ita ala doli kunya.

Wani daɗi ya luluɓe zuciyar Alhaji Waleed ya samu mace ta gari mai kunya,cikin nuna ƴar damuwa ya kuma cewa "to bbna Allah matso lokacin da wuri ungo ga wannan kin sayi hoda"ya miƙa mata kuɗi amman Nabee ƙememe taƙi karɓa kamar kullum.
Hannunta ya jawo ya saka mata kuɗin, tsabar jaraba sai da yaji wani abu daga haɗuwar hannunsu.

A kunyace ta jimƙe kuɗin ta na godiya "Allah saka da alkhairi ya biya ka da gidan aljanna mafi ƙololuwa"Alhaji yayi murmurshi haɗi da jin daɗin addu'arta yace "haba ai babu godiya a tsakanin mu"ta ƴar dariya gami da fari da ido kafin ta gyara dogon hijab ɗinta ta fita daga mota.

Turus tayi tsakar gida ganin Iyani ta saka Nasir a gaba ta na zagi shi kuwa ya sunne kai "ai yanzu sai ka tashi ka sawo rago dan ni kuwa ko ƙwandala ta a to😏 a bar ni da baƙin cikin wacan asararar kawai ina dalili kai kaje ka ɗirkawa ƴar mutane ciki ni ma an zo an yiwa tawa Ƴar masifar ka ce ka zoza mata"shi dai Nasir bai ce komi ba har sai da ta gama sannan ya miƙe ya bar gun.

Can tsakar dare ciwon mara da azaba iri-iri suka ishi Fauziya ta miƙe zaune ta na sharar hawaye.
Kallon Nabeela ta tsaya yi wacce ke sharar barcinta hankali kwance,wani irin da na sani ne ya wanzu a zuxiyarta kawai sai ta fashe da kuka.

Cike da masifa Nabee ta tashi daga barcin da ke,ba tayi wata-wata ta ɗauke Fauziya da mari ta na cewa "minene?uwar miye ki kewa kuka yanzu tsakar dare?"cikinta Fauziya ta nuna wanda sai ƙara yin ƙasa ya ke.

Tsuki Nabee tayi tace "uban wa ya aike ki mtws wawuya kawai"tayi kwanci babu jimawa kuma wani barcin ya ƙara ɗauke ta.

Wata irin azaba ce Fauziya ke ji ta ko ina sai dai ba ta da iko ko halin yin wani abu,ko kafin gari ya waye ta jigata tuni ruwan waya sun fashe su na ta zuba amman babu mai kula da ita.
Nabee na sauke ƙafarta da asubah taji danshi waro ido tayi da sauri ta cire sakata ta nufi ɗakin Iyani ta na kiranta.

Nasir ya nemo mai taxi suka wuce asibiti,ba su jima ba kuma aka tura su babban gida wato likita babba.
Da isar su Mère et enfant aka wuce da ita Bloc saboda matsalar da suka hango,tayi doguwar naƙuda ga kuma ƙarancin shekarunta.
Ko da aka ciro yaron bai zo da rai ba,ɗakin hutu aka kai Fauziya.
Hamdallah Iyani tayi da aka ce jaririn ya mutu sai dai kuma result ta biyu ta tayar mata da hankali na kamuwar yoyon fitsari da Fauziya ta samu.

***

Sharkaf na haɗa zufa saboda turaren hayaƙin da Momy ta sa ni ala doli sai nayi,ina buɗe bargon wani ƙamshi ya game ɗakin yayinda fatar jikina ta ƙara yin wani haske gami da kwantawa da taushi.
Toilet na wuce,ruwan da aka haɗa min cikin bawon wanka na shiga ina mai lumshe ido jin ɗuminsu ya ratsa ni ga wani ƙamshi da suke fitarwa.

Humra na shafa a duk wani lungu na jikina kafin na saka kaya,Momy ta shigo hannunta ɗauke da tray yayinda Yayunta mata biyu ke take mata baya uwanda sun zo ne saboda bikina da kuma taya murnar dawowata.

Baki na kwaɓe dan har ga Allah na fara gajiya da shaye-shayen nan, murmushi Momy tayi ta fara miƙo min ina shanyewa ina bata kofin Allah ya so ni wannan karon duk maganin zaƙi ne da su.

Wayata ta ɗauki ringing ƙin zuwa nayi kusa da wayar balle na ɗauka domin ringing ɗin Daddy ne kuma yanzu da na ɗauka zai fara shagwaɓe min ya na min zantukan da sun girmi lissafina.

"Ba ki jin ana kiran ki ne?"cewar Momy turo baki nayi nace "Daddy ne" "to ki ɗauka mana ki koma can falo"ta faɗa ta na mai nunawa Yayun nata wasu kaya su kuma suna dubawa.

Wayar na cire daga caji na fita sannan na ɗaga ina mai karawa a kunne wani irin numfashi ya sauke wanda yasa zuciyata yin wani yarrr kamar an tsagata "jj-2 jours dai na matsu"shine abinda Daddy ya faɗa "wai yanzu banda gobe ne auren?"na tambaya ina waro ido "ƙwaran gaske nan da jibi kin zama tawa yauwa faɗa min abinda kika tanadar min"....
[12/12 à 10:37] Cham~rose💞: *LITTAFIN KUƊI NE KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE,DUK WACCE TA KARANTA MIN BOOK KYAUTA DA WACCE TA TURO DA WADDA TA GAN SHI A WANI GROUP ITA MA TAYI SHARING IN KUN YI DAIDAI KUN SANI🤷🏻‍♀️ mai son biyan kuɗin karatu sai ta tuntuɓe ni ta WhatsApp* +22795045822

*Page 43-44*

"Ni ban san mi na tanada ba"na faɗa cike da ƙurciya murmushi yayi mai sauti yace "to naji wane Gift kike na baki a matsayin tukuici?"ba tare da wani tunani ba nace"mota ni ke so fara sol mai kyau irin ta mata sai kuma Teddy da kuma farar mage"dariya Daddy ya kece da ita ni kuwa na turo baki nace "Allah su ni ke so Daddy ko ba za ka saya min ba?"
"Haba Mimi mi za kiyi da mage?sannan ni ina zan ga farar mage?"Daddy ya tambaya.
"Nemowa za ka yi mana,kuma fah na ga hoton wata mage cikin wayar mai kyau"Daddy yace "to ko ciro hoton ake sai a maki cadre ɗin sa?"na waro ido waje tamkar ina gabansa nace "hoto?hoto kuma Daddy?to miye banbancin da na cikin wayar tunda shi ma ba motsi zai yi ba ?ni dai ta ƙwarai ni ke so"na fara bubuga ƙafafu ina kukan shagwaɓa.
"Ya Salam!"Daddy ya furta jin wata kasala na zubo masa tamkar yayi ihu saboda abinda ya ke ji duk jikinsa.

"Shuuut!"ya faɗa a kasalance kafaɗa na maƙe kamar wacce ya ke gani nace "ni dai a'a sai kayi alƙawalin za ka samo min" "naji shikenan ko?"Daddy ya faɗa ya na furzar da huci.

Murmushi nayi mai sauti nace "yauwa Daddyna na gode,ina Hajiyar mu?"
Ya bani amsa da "ta na can falo" "kai kuma fah ka na ina?"na tambaye sa ina lumshe ido saboda a yadda ya ke sauke numfashi ya jefa ni cikin wani yanayi "ɗakina"ya bani amsa na kuma tambayar shi "ka na mi?"
"Kwance mana"shiru nayi jin yadda numshinsa ke sarƙewa "to kaima Hajiya Babba wayar ina son mu gaisa"na faɗa a Shagwaɓe dan naji kamar barci ya ke son yi.
"Ban iya fita a wannan halin"ya bani amsa,na turo baki nace "wane hali kuma?"kai ya girgiza a zuci kuma yace "oh Mimi yanzu ba ki gane halin da na ke ciki ba sai kace yarinyar goye?"kukan shagwaɓa na saka mashi jin ya ƙyale bai ce komi ba.

"Babynaaa"Daddy ya furta cikin wata irin murya wacce ta sa doli na nutsu "uhum"
"Minene ?"na kwaɓe fuska kamar zan yi kuka nace "komi ni cikina mai ke ciwo"Daddy ya gyara kwanciya yace "daidai ina?"na bashi amsa "ga ciki mana"
"Na sani ga ciki,amman saman ciki ko ƙasan shi?"wata kunya ce naji ta kama ni wlh kawai sai nayi ƙasa da murya nace "a'a ba daga sama ba"

Ya sauke ajiyar zuciya yace "to naji Allah baki lafiya"nace "amen!ina Hajiya Babba ɗin?"Daddy ya dafe kai yace "Mimi sai yaushe za ki barin rigima ?a wannan halin zan fita kaiwa Hajiya waya?"cikin rashin sanin manufa nace "to mi ya ke yi?"
"Bai komi bari ranar da kika zo za ki gane" "naji to sai an jima zan ci abinci" "ok ki ci dayawa"
"Toh"na bashi amsa shi kuma ya kashe wayar.

***

Cikin kuka Mami tace "Dr Ibrah sam wannan ba halin ƴaƴan musulmi ne ba,ta yaya babu igiyar auren ka ko ɗaya a kaina amman kullum sai ka zo min?haba ka bar ni na sarara mana da wane zan ji da wannan ƙaddararren cikin koko da jarabar ka?"kwasheta yayi da mari ya nunata da yatsa yace "ki iya bakin ki in ba haka ba zan yi maki shegen dukan da duk wanda ya gan ki sai ya tausaya maki"shiru Mami tayi ta kasa cewa komi yayinda shi kuma Dr Ibrah ya fara yamutsata.
Kafin wani lokaci kukan da Mami ke yi ya sauya zuwa ihu🙊
Ameera wacce ke falo zaune ta tashi ta leƙa su ta ƴar hudar ƙofa ( *KE DUNIYA* next book ɗina in shaa Allah wanda zai magana akan sakacin iyaye masu sex ƴaƴan su na ji)

Da sauri ta ja da baya ta na waro ido tabbas irin abinda ta ke kallo a waya ne su Mami ke yi,tunani ta fara inda za ta samu mafitar abinda ta ke ji.
Hijab ta saka ta fita waje mai adaidaita ta tara ta kwatanta mashi inda zai kaita,suna tafe mai adaidaita na saurarren wa'azin Malam Bashir Ghana inda ya ke cewa ```«Yarinya budurwa ki tsare kan ki saboda a ranar lahira gangar jikin ki zai bada shaida da irin abubuwan da kika yi,farjin ki zai bada shaida iya adadin mazajen da suka yi zina da ke,ƙirjin ki zai yi magana iya adadin samarukan da suka taɓa shi,laɓan ki za su bada shaida akan duk namijin da ba mijin ki ba da ya taɓa kissing naki,ƙafa za ta bada shaida ce a ranar ni na taka ta je wajen,Saurayi ma haka a gaban ka za kaji azakarin ka na baiwa Allah report iya adadin matan da kayi zina da su,bakin ka zai ce ni nayi kissing nata hannu yace Ni na taɓa.Dan haka samari da ƴan mata

kuyi hattara kuyi taka tsantsan da zangon ƙurciyar ku zango ne da babu sauƙi saboda a lokacin ne kuke da ƙarfi kuke ganiyar samartaka ku saboda rayuwa ta kasu zango uku ne,YARINTA,SAMARTA,TSUFA babu zangon da ake tsananta bincike kamar na tsakiya saboda wannan lokacin Allah ya baka ƙarfi fiye da zangon biyu wanda suke tattare da rauni»``` a daidai nan Ameera wacce jikin ta duk yayi sanyi ta sauka tare da biyan mai adaidaita.

Kallon gidan saurayin nata tayi wanda shine ke tura mata blue Film,kawai kuma sai ta fashe da kuka ta na girgiza kai a fili tace "ai babu babban tonon asiri kamar Allah ya tsare ka gaban bainar nas ana bincikar ka tare da bankaɗo mugan halayen ka, Allah na tuba ka yafe min nayi alƙawarin ba zan taɓa barin idona ya kalli haram ba sannan zan zama mutumniyar kirki ta yadda Manzon Allah SAW zai yi alfahari da ni a ranar alƙiyama"ta na tafe ta na jaddada tuban ta gun shugaban talikai babu zato kawai sai ji tayi an kwasheta ta faɗi ƙasa daga nan kuma ba ta sake sanin abinda ya faru ba.

A ruɗe  ABU MALEEK(Nimcyluv)ya fito daga mota ya na mai furta "Innalillahi wa'inna iley raji'un"sungumarta yayi ya saka bayan mota ya na mai tambaya inda zai samu asibiti nan kusa,nan wani ya kwatanta mashi.

Da isar sa Clinic Khasum Moctar aka shiga dubata,ashe suma ne tayi saboda furgici sai kuma kanta da ya bugu an wanke gun a naɗe sa da bandeji.
Shiga yayi ɗakin da aka shimfiɗe ta,tsayawa yayi ya na kallon ƙyaƙyawar fuskarta da hawaye ke shatata daga cikin manyan idonta masu dogayen gashi.
Ƙarasawa yayi ya saka hannunsa mai dogayen yatsu ya fara goge mata hawayen sai dai wasu kuma ke sake zubowa,"ya Allah!"ya furta a hankali cikin muryar shi mai sanyi buɗe idonta tayi suka sauka kan chocolat face ɗin shi mai ɗauke da jan leɓo.

Maida idon tayi ta rufe ta na tunanin abinda ya faru da ita,"buɗe idon ki petite beauté"ya faɗa ya na mai ɗaga fatar idonta wanda yasa doli ta buɗe su "ya jikin ki?"ya tambaye ta,samun kanta tayi da murmusawa kawai shi ma sai yayi murmushin yace "mi sunan ki?"
"Ameera"ta bashi amsa "Meera,ni sunana Abu Maleek yau ɗin nan na shigo garin Maradi cike da zumuɗin zan je na ga ƴar little sis ɗina da aka gani ga shi kuma gobe za'a ɗaura aurenta sai kuma Allah ya katse min hanzarin na banke petite beauté"ya na maganar ne ya na murmurshi mai nuni ya na cikin farin ciki sai kuma da ya zo ƙarshe ya kwaɓe fuska.

Murmushi Ameera tayi ta yunƙura za ta tashi da sauri ya taimaka mata "yi a hankali,bani number wani ɗan gidan ku sai na shaida masa ki na asibiti kar aje ayi ta neman ki"ai tamkar ya caka mata wuƙa haka Ameera ta shiga rera masa kuka.

